[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: *GJSR*
*77&78*
*PROBLEM!*
Sakamakon tsintar gawar matashiyar budurwa a bakin hanya ya tashi hankalin duk wanda ke zaune a cikin 'kauyen *KUYAN TA INNAH!* saboda abu ne dai ta'ba faruwa ba, shiyasa hankali kowa ya tashi mussaman maigari da uban yarinyar, cikin tsantsar tashin hankali da damuwa suka nufi cikin gari domin sanar da hukuma don ta gabatar da binkice akan gawar yarinyar da kuma abunda ya janyo mutuwarta.

A nan binkice ya nuna cewa fyad'e akai mata wanda ya janyo har ta rasa rayuwarta, maihafin yarinyar dai kasa daurewa yayi kawai ya zube a gaban gawar yana share hawaye hakika wanda ya aikata wannan ta'annati ya cika mara imani, mara tsoron Allah domin kuwa idan ba mai bushewar zuciya ba to babu wanda zai aikata wannan mugun ta'addanci...........Duk binkicen da ake gudanarwa an kasa gane wanda ya aikata mummunan aikin, domin wanda ya aikata mugun abun dashi da jama'arsa dasu ake gudanar da binkicen kuma suna sawun farko gurin nuna alhininsu da kuma tashin hankalinsu, domin dai dasu din ake binkice shiyasa babu wanda ya d'ora zarginsa a kansu domin duk sun rufe wata kafa da zata nuna cewa su d'in bara gurbi ne a cikin al'umma.
Wannan al'amari ya girgiza jama'ar dake cikin wannan 'kauye kasancewar abu ne da bai ta'ba faruwa ba, sai dai su ji labarai a redio da sauran kafafan sadarwa.

******
Cikin nutsuwa da kwanciyar hankali ya gama cinye hutunsa ya fara shirye-shirye komawa bakin aikin...........A cikin kwanakin da sukayi a tare sun d'an samu jituwa da juna sun rage fad'a kusan koda yaushe suna tare idan dare yay kuwa sai sunyi romancing din junansu suke jin dadi wannan shine mataki na farko da ya janyo musu samun jituwa a tsakaninsu.

Wani irin so take masa a can kasan zuciyarta, wanda take jin bala'in kishin duk macan da zata kusance shi, sosai da sosai ta sanya ido a kan sa da duk wani motsinsa.........Ganin haka yasa shima ya kiyaye baya amsa kiran Hamra'u a gabanta, amma suna tare da juna kuma har yanzu da akwai kudirin auranta a zuciyarsa.

Tana sonsa amma ta kasa nuna masa son a aikace, ta sake shi sasakai bata san ci da shan sa ba, ba tasan idan ya dawo daga aiki ta masa sannu da zuwa ba, ba tasan tayi masa kalamai masu dadi ba, akwai gyara masu yawa a cikin al'amuranta.......Yanda ya fahimceta ita kawai su shiga bargo daya suyi romancing shine abunda take so a gare shi, wanda shi kuma a nasa bangaran ba haka yake da bukatar rayuwar auransu ya kasance ba, yana so ta zama *Mar'atussaliha* wato mace tagari mai ladabi da biyyaya da kuma kiyaye dokokin ubangiji.

Tun yana yaro yake da burin auran nagartacciyar mace mai hankali da nutsuwa da sanin ya kamata, sai gashi kuma hakan bai samu ba, wacce Allah ya had'ashi zama da ita tana da nakasu a kowane 'bangare, domin ba ta cika addininta ba, ballanatana ta san meye hukunce-hukuncen aure..........To wannan shine dalilin da ya sanya yake da burin auran

Hamra'u domin duk ta tara abubuwan da yake da bukata, amma kuma a can k'asan zuciyarsa ya fi jin uwargidan nasa.

Lafiya kalau suka rabu ya fita daga aiki, ta koma sashenta cikin farin ciki da annushuwa yanzu ta manta da boyayyan masoyinta tunda tana samun abunda take kulafuci a gurin mijinta, shiyasa ko ya turo mata da text bata kula shi dama a rashin uwa akanyi uwar daki.......Ta iske hadimanta na aikace-aikace a falon, suka zube har kasa suka gaisheta kafin ta wuce ciki........Shigarta dakin da minti biyar Marakisiyya ta shiga, ta kalleta da fadin." Lafiya."?

Sunkuyar da kanta tayi kafin tace." Ranki ya dade ni kam wannan al'amari ya ishe ni wallahi, shiyasa kawai na yanke shawarar fada miki domin kiyi wa tufkar hanci."

Gabadaya ta mayar da hankalinta gare ta da fadin."Marakisiyya fada min ko meye."?

Tace." Kullum sai bayan kin fito daga can bagaran maigidanki ita kuma nake ganin gilmawarta a gurin ban san me yake kai ta ba, ranki ya dade ya kamata ki tsawatar mata."

Gabadaya yanayin ta ya sauya gabanta banda faduwa babu abunda yake kishi ya rufe mata ido tace." Wai kina nufin Hamra'u ko kuma wa."?

Tace." Kwarai ranki ya dade ita nake nufi kullum da safe sai ta shiga sashen."

Wani irin gumi ya fara karyo mata mussaman a saman hancinta.

Tsaye ta mike ta gyara lifayar dake jikinta, hanyar fita ta nufa ranta a masifar 'bace!

Aikuwa a bude ta samu sashen bayan tare suka fito dashi ya rufe har bakin mota ta raka shi sai da ta tabbatar da cewa ya fita daga Barack din sannan ta nufi gurinta , ashe munafurtar ta suke, a'ina yarinyar ta samu key din gurinsa.

Ta tura dakin ta shiga ido suka had'a tana tsakiyar gadonsu da sunan tana gyarawa, ganin Gimbiyar yay bala'in gigita ta, mara gaskiya ko a ruwa gumi yake, itama ta san abunda take bata kyautawa amma ta na yin hakan ne domin ta kafa gwamnatin ta.

Ta sakko daga gadon da rigar fillo a hannunta, a sanyaye tace." Aunty Ina kwana."?

Ba ta amsa ba, ta nufi inda take cikin tafiyar isa da k'ama.!

Ta daure ta tsaya domin bata tsammaci cewar hukuncin mari ne zai biyo bayan zuwanta gurin ba kawai taji saukarsa a kumatunta, ta zabura! ta dafe gurin da fadin." Me nayi miki zaki mare

ni."?

"Ubanki ki kayi min."! tafad'a jikinta na wani irin rawa!!

Ta nuna kirjinta da fadin." Ubana fa ki kace."?

Tace." Eh don ubanki! waye ya baki ikon shigo min turakar miji."!

Ranta ya 'baci! tace." Kada ki kara zagina domin idan ki ka sake zan rama turakar mijinki kuma dama tun kafin kizo gidan nake shigowa ina gyara masa saboda haka ke baki isa ki hana ni shigowa ba."

Tace." Ban isa na ha naki shigowa ba."? kai ta gyada alamar E.

Tarin belt din da suke rataye a jikin hanga ta fizgo daya, kawai ta shiga zabga mata a jiki ta ko'ina.................. Wannan shi ake kira ba zato! ba tsammani, Hamra'u da gudu ta fice daga dakin, itama ta bita da gudun tana cigaba da zabga mata blet din da fadin." ' Yar iskar yarinya mara kamun kai kawai ni zanyi maganin ki duk sanda na k'ara ganin kafarki a dakin nan sai nayi miki abunda yafi haka."
Hamra'u na kukan bakin cikin ta isa sashensu kawai sai ta zube a kujera tana rusa ihu! kafafunta da saman wuyanta shatin belt rad'au! ya fito..
Jin kukanta yasa Uwale fitowa daga daki, hankali a tashe take tambayarta abunda yake faruwa.

Kasa yi mata bayanin komai tayi ta tashi ta shige d'aki tana share ha waye.......Wayarta ta dauka ta kira shi...........Ya daure ya bar abunda ke gabansa ya daga wayar, jin alamun kuka a tare da ita ya sanya shi mamaki yace." Hamra'u menene ya faru kike kuka kiyi shuru kiyi min bayani."

Da k'yar tai shuru tana sauke ajiyar zuciya ta shiga sheda masa irin cin mutuncin da matarsa tayi mata.

Ransa a 'bace a kan me ta dauki belt ta zane ki, ke kina me har zaki zauna ta doke ki."

Hanci ta shaka kafin tace." Kawai dan ta same ni a dakin ka ina gyarawa shikkenan tayi min wannan cin mutuncin."

Yace." Kiyi hakuri wannan ba hujja bace, kuma idan na dawo gidan zanji dalilinta nayi miki wannan tozarcin! saboda haka kiyi hakuri insha Allah zanyi maganin abun."

Ajiyar zuciya ta sauke da fadin."Shikkenan tunda kace haka Allah ya dawo da kai lafiya."

Ya amsa da "ameen ya Allah kafin ya kashe wayarsa."

Sosai ransa ya 'baci da abunda tayi, a ganinsa ai ba wani abu bane, tunda ita ta kasa d'aukar ragamar ayyukansa to bata da hujjar da zata hana wani yayi masa hidima dole ya nuna mata kuskuranta idan bata so wata mace ta kula dashi to tayi gaggawar gyara kuskuranta.

Yana ganin kiran wayarta yaki d'auka,  ta kira ya kai sau goma amma bai daga ba,  hankalinta ya tashi mutuka domin ta tsani ta kira waya a share ta a ganinta da gayya yayi mata hakan.

Hawayen takaici ta share kafin ta kira Aunty Zeey sama-sama  suka gaisa da juna, ashe kowacce da abunda yake damunta aunty Zeey din ce ta fara yi mata complain akan Madam uwargidanta sai d'ura mata ashar  take  tare da fadin." Ta asirce Asp din sai abunda tace  yake aikatawa.

Ta sauke ajiyar zuciya da fadin." Aunt Zeey ni a ganina naki mai sauki ne tunda kishiyarki ce kuma ke kika sameta a gidan, ni kuwa fa wata 'yar iskar yarinya 'yar 'kauye tana cin dunduniyata ban sani ba, ashe kullum tana tare da mijina kamar matarsa   tana zuwa sashensa ta hau gadonsa da sunan gyara wannan abu ya 'bata min rai mutuka da gaske."

Aunty Zeey din ta dinga kurma ashar kamar bamagujiya tace." Kici uwar shegiya!  wallahi kada ki saurara musu gabadaya ki tashi hankalinsa har sai kinji abunda yake tsakaninsu."

Ta ciji yatsa da fadin." Aunty Zeey  ni kadai na san irin bala'in da za muyi a yau wallahi sai naji dalilin zamanta a gidan nan sannan zai sheda min dalilin da ya ha nashi daukar waya ta."

Tace." Yaushe kuwa zai dauki wayarki  bayan ta ki rashi ta sheda masa karya da gaskiya.........Kada ki saurara musu wallahi."

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke  cikin ranta take raya irin dambarwar da zasu buga idan ya dawo gidan.

Tsaf ta shirya tayi gayu cikin wata dakkakiyar shadda dinkin sinigal aiki a ko'ina wuya hannu da kasan rigar, ta zuba gold a ko'ina hatta da yatsun k'afa  babu wani cikakken kwalliya a fuskarta amma tayi wani bala'in kyau tamkar fure kowane dressing tayi yana kar'bar jikinta.........rufaffen takalmi tasa a kafafunta ta  yafa mayafi irin na sarauta  kai tsaye sashen nasa ta nufa tana zabga k'amshin turare  fuskarta babu walwala ko ta gamin gafara.

Bai dawo ba tukkuna ta samu kujera ta zauna tana cika da batsewa sa'i da lokaci tana kallon agogo wani sa'in shida na yamma a gida take masa amma yau har ta gota shiga da ashirin bai shigo ba.

Ta mike kai tsaye window ta nufa, tana daga labulan motarsa na shigowa barrack din.............Ta sauke ajiyar zuciya tare da kurawa motar ido har ta isa gurin da aka tanada domin ajiye motoci.

Direban shi ne ya bude masa motar kafin ya fito da wasu takardu a hannunsa, ya tsaya suna magana da direban kafin ya bashi hannu sukayi musabaha da juna.

Labulan ta saki ta koma ta zauna kan kujera tana tsumayin shigowarsa.

'Kamshin turaranta ne ya daki hancinsa, ya dan lumshe idonsa kafin ya bude ya saukesu a kanta tana hakimce! 'kafa daya kan d'aya.

Abunda yake 'kara rikita shi a kanta gayu da iya ado yana san irin kwalliyar da take masa.......Munanan halayenta ne kawai abun gudu.

Yanayin sa ya gyara domin shi din ma bai shigo da wasa ba, ya bude baki yayi sallama cike da karsashi! da kwarin gwiwa!

Ta amsa a ciki kamar ba taso.

Bai saurareta ba kai tsaye bedroom d'insa ya nufa ba tare da ya kalli inda take zaune ba.

Tayi 'kwafa tare da bin bayansa.

Yana kokarin cire uniform din jikinsa ta shiga ta same shi, ya kalleta itama ta kalleshi dauke kansa yay yaje ya rataye kayan, toilet yake kokarin shiga maganarta ta katse shi.

." Ina so zanyi magana da kai."

Ya juyo ya kalleta na second biyu kafin yace." Ina da uzuri a gabana yanzu sai an jima tukkuna."

Wani malolon abu yazo ya tsaya mata a wuya! ko kafin ma tayi wani yunkuri ya shige toilet ya bar ta da b'acin rai!

Koda ya fito bai kalli inda take ba ya fara hidimar shirya jikinsa, yana jin ciwon yanda ta bar shi

sasakai komai shi yake wa kansa.

Ta iske inda yake cikin bala'i! da neman fitina! tace." Kasan abunda ya faru shiyasa kake wani dauke kai saboda rashin gaskiya, to da kai da yarinyar duk zanyi maganinku dan bana shiri da munafiki."

Ya kalleta da bacin ran maganarta yace." Eh na san irin rashin mutuncin da ki kayi wa 'yar mutune me ta tsare miki daga gyara kayan ki zaki dauki blet ki doke ta, meye hujjarki ta aikata hakan"?

Tana numfarfashi! tace." Saboda ta shigo min turakar miji shiyasa nai mata wannan hukuncin kuma wallahi ko yau ta sake shigowa dakin nan sai naci ubanta."!!

Ya ja mata tsaki! tare da kokarin ratse ta ya bar gurin......Tare shi tayi har jikinsu na had'uwa......Murya na rawa tace." Wallahi ba zan yarda da wannan munafurcin ba sai ka fada min tsakaninka da ita domin tun baya yau ba na fahimci akwai wata alaka a tsakaninku."

Ya jima yana kallonta da tsananin 'bacin rai a tare dashi yace." Kin ga *ZINA* bana bukatar 'bacin rai a yanzu kada kiyi sanadin da zai janyo mana samun matsala, tsakanina da Hamra'u idan lokaci yayi zaki sani."

Tace." Bana jin tsoro ko shakkar 'bacin ranka munafurci ne bana so kawai ka fad'a min abinda yake tsakaninka da ita idan babu wata alaka to wallahi sai ta tattara kayanta ta bar gidan nan domin zamanta bashi da amfani."

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ke baki isa kisa Hamra'u ta fita a gidan ban ba, domin tun kafin ki zo muke zaune da ita, alakar dake tsakanina da ita kuma lokaci ne zai nuna miki."!

Ta fashe! da kuka tana dukan kirjinsa da fadin." Wallahi na fad'a maka sai dai ka za'ba koni ko ita domin ina zargin wani abu, wallahi kaji na rantse da Allah ba zan hada kishi da ita ba."

Tana kuka sosai take maganar tana kuma cigaba da dukan kirjinsa!

Gabad'aya jikinsa ya mutu ya dinga kokarin rik'e hannuwanta ta fuzge da karfi! ta kama hanya da sauri ta fice daga dakin tana share hawaye........Gefan gado ya zube tare da dafe kanshi.......Hohoho!! *ZINATU PROBLEM!!😃*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: *GJ*
*79&80*
Ya jima dafe da kai yana tunanin hanyoyin da zai bi gurin ganin ya kawo gyara da zaman lafiya gidansa, maganar gaskiya dole yarinyar nan ta gyara kuskuranta mutukar tana so ta zauna lafiya dashi to  tilas ta kula dashi da duk bukatunsa, amma baya tsammanin zai hana Hamra'u hidima dashi mutukar ita din ba tayi wani abu akan al'amarinsa ba, idan yaga ta mayar da hankali gurin bashi kulawa to  da wayo da dubara zai iya dakatar da ita Hamra'un akan abunda take  cewa ta bari tukkuna har sai an daura musu aure.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke  yana yun'kurin tashi kiran Asp ya shigowa wayarsa, sai ya koma ya zauna yana laluben wayar a cikin aljihun rigar dake jikinsa.

Sam bai tsammaci jin maganar daga gare shi ba kawai sai yaji yana tuhumarsa akan abunda ya faru a tsakaninsa da yarinyar.

Ransa yayi mutukar baci da jin irin tuhumar da Asp din yake masa dan haka sai yayi saurin katse shi a kaurare yace......."Asp kada fa ka manta da cewa wannan yarinya da ake magana akanta itace za'bi na tuntuni ita nake da ra'ayin aure kafin maganar Gimbiya ta sanyo kai, mai yasa kullum idan yarinyar nan zata kawo maka k'orafi baka bin ba'asi idan an bi ta 'barawo to abi ta mabi sawu, yarinyar nan  har yanzu bata cika mace a gidanta ba, domin kuwa akwai sangarta da lalaci a tare da ita, duk wasu hanyoyin kula da miji ba ta san su ba, shin laifi ne dan Hamra'u tayi min hidima? dama can ita take kula dani kafin wannan al'amari ya faru saboda haka don Allah mu bar maganar nan domin kai kanka kasan gaskiya kake takewa saboda gudun bacin ran mara gaskiya."

Asp din jikinsa yayi sanyi yace." Umaru duk abunda ka fada gaskiya ne to amma ba kayi la'akari da gidan da yarinyar nan ta fito, kasan dai gidan sarauta ba komai sukewa kansu ba, komai yi musu ake dole ta samu na'kasu ta wannan bangaran, ba wai ina goya mata baya bane nima nasan gaskiya, amma lamarin mata akwai rikici bana so wannan matsalar ta hargitsa maka gida domin 'karamar magana tana iya zama babba! shine dalilin da yasa nake baka shawara kayi wa tufkar hanci tun kafin lamari ya 'baci  abunda nake nufi anan shine ita Hamra'u ta janye jiki daga duk wani abu da ya shafe ka ta bari tukkuna ku mallaki juna ina ganin shine maslaha a tsakaninku."

'Karamin tsaki yaja da fadin." Asp dacewa ne ace yarinyar nan ta d'auki belt ta zane yar mutane

dashi? ko kuma dacewa ne ace ta bar gurin da nake kwanciya kaca-kaca babu gyara,  kana maganar daga gidan sarauta ta fito mata nawa ne suke da sarautar amma suna tsaye akan mazajensu da kulawa dasu.....Na tabbatar da cewar duk irin rashin mutuncin da yarinyar nan take tana sane, tunda ta san taci abinci tayi ado da kwalliya dare yayi ta nemi biyan bukatar ranta  to mai zai sanya ta kasa aikata ayyukan da ta san zasu faranta min rai, Asp ina son yarinyar nan sosai amma dole na auri wacce ta san mutuncina dana 'yan uwana wannan shine hukuncin dana yanke."

Yace."Nima ban ha naka aure ba Umaru kawai ina baka shawara ne akan ka yi saurin gyara al'amarin kada ya 'baci, hakika abinda tayi bata kyauta ba,  wannan dalilin yasa nake baka wannan shawarar."

Yace."Shikkenan nagode sosai insha Allah zanyi kokarin ganin komai ya daidaita."

Yace." To alhamdulillhi nagode da daukar shawarata."

Sallama sukayi kowanne zuciyarsa cike da damuwa, mussaman shi Umar din da yake ganin kamar yarinyar tana nema ta dinga fitar masa da sirrin gidansa, duk yanda yake da Asp din baya bukatar yaji abunda ya shafi iyalinsa, ai ko babu komai sirri yana da dadi.

Side din ta ya nufa,  ya same ta kwance a gado taci kuka ta koshi kwayoyin idanuwanta duk sun sauya kala.

Kallo d'aya tai masa ta kawar da kanta tana zumb'ura baki.

Shi kam tsigar jikinsa ce ta tashi! ganin yanda idanuwanta sukayi jajawur! hakan ya daga masa hankali mutuka!  wannan ya tabbatar masa da cewa tana sonshi tunda har take kishi a kansa.

Ya zauna kusa da ita da fadin." Tashi muyi magana."

Share shi tayi ta juya masa baya.

Ya rike hannunta yana kokarin tayar da ita tana komawa.

Kusa da ita ya kwanta ya janyota jikinsa sosai  hannuwansa duk biyun yasa ya ratsa jikinta.........Ajiyar zuciya suka sauke a tare.

Kimanin minti goma ya kai yana kokawa da zuciyarsa kafin ya daidaita nutsuwarsa ya fara magana kamar haka.

"Me yasa zaki shedawa Asp sirrin gida na."?

Kai tsaye tace." Saboda shi kadai zan shedawa abinda yake damuna ya rarrashe ni."

Yaji wata kibiyar kishi ta soki makogwaronsa! yace." Kwanakin baya fa haka ki kayi min na gargade ki kan cewa bana so kina fita da duk wani abu da ya faru a tsakaninmu shin mai yasa ke ba zaki zama mace mai sirri da rike amanar mijinta ba."

Da sauri ta mike zaune tana masa wani irin kallo tace." Yaushe ka bani damar hakan, bayan kullum kana munafurtata kana tare da yarinyar nan kuna mu'amula tamkar mata da miji, a ina ta samu key din sashenka? sannan meye hujjar ta na hawa gadonka, koda yake ban sani ba ko kana biyan bukatarka da ita."

Ya dinga kallonta yana auna maganganunta......Maganar da tafi daukar hankalinsa "Ko da yake ban sani ba ko kana biyan bukatarka da ita." Wannan maganar ta bashi mamaki mutuka."

Yace." Yanzu me ki kike nufi da wannan maganar? me ki ka dauke ni fasiki kome."?

Ba tare data kalleshi ba tace." Duk abunda zuciyarka ta raya maka hakane a zuciyata."

Ya sauke zazzafar ajiyar zuciya yana kokarin danne bacin ransa, baya so ya biye mata su zo suna hayaniya shiyasa yake bawa zuciyarsa hakuri, ya tashi zaune tare da kokarin rike hannunta tana fuzgewa.

Yace." Ni Sulhu nazo muyi ba wata hayaniya ba, wannan maganar da ki ka fada a kaina ta 'bata min rai fiye da tunaninki amma ina so ki san wani abu da ni din mazinaci ne ina ganin da tuni kin sheda hakan tun a haduwar mu ta farko na samu dama iri-iri a kanki amma ban cutar dake ba, ki sani cewa yanda na tsani zina haka na tsani mutuwa ta, kullum cikin nesanta kaina nake da ita to mai zai sanye ki dinga alakanta ni da aikata hakan me nai miki ? ko kuma kina so ace mijinki ya kasance mazinaci ."?

Shuru tai gabadaya jikinta yayi sanyi da kalamansa .

Ganin haka yasa yace." Maganar Hamra'u muke a yanzu ba kya so ta cigaba da kula dani to kiyi gaggawar gyara kuskuranki, abun nufi anan shine ki dauki ragama ta da duk wani abun da

ya shafe ni, ina nufin ci da sha na da kuma tsaftace makwancina ladabi da biyayya, sai kuma abu na karshe bani hakkina na aure wannan shine abubuwan da zakiyi wanda zai sa Hamra'u janye jikinta dani."

Ajiyar zuciya ta sauke tare da d'an zumbura baki  abunda ya zame mata jiki,  tace." Ni a guri na duk wannan mai sauki ne, burina kawai ka fita daga sabgar yarinyar domin bana bukatar wata mu'amula ta shiga tsakaninku,  kawai ta tattara kayanta  domin bana bukatar ganinta a in da nake."

Yace." Wannan ne kuma ba zai samu ba, na fada miki tun kafin kizo gidan nan yarinyar take, tun muna 'kauye muke tare tayi min hidima sosai kana kulawa da kakata babu dalilin da zai sanya ta bar gidan nan babu kwakwkwaran dalili."

Wani irin kallo tai masa mai kama da harara  kafin tace."Wai shin ma meye dangartakar dake tsakaninku."?

Yace." 'Yar 'kanin Uwale ce a matsayin 'kanwa take a guri na."

Tace." Bayan wannan ala'kar ai  akwai wata dan ba zan mance ranar da kake shedawa Asp ita a matsayin wacce zaka aura ba shin ko ba haka bane."?

Da yake yana bukatar maganar ta mutu sai kawai yace." Wannan ai tsohon zance ne ki ajiye shi a gefe ke dai kawai ki gyara kusakuranki sai mu zauna lafiya, amma ki daina k'yamar ahali na."

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin sassauci a cikin zuciyarta,  tace." Idan ka rike min alkawari nima zan baka mamaki."!

Murmushi yayi wanda yake fito da zahirin kyawunshi yace."  Kada ki damu amma wane irin tanadi ki kayi min yau domin ina tunanin  angwancewa  kin shirya ko."?

Jin abinda yace  yasa tayi masa wani irin kallo,  ya daga mata gira gami da so ya tabbatar mata da maganarsa.........Gabadaya jikinta  sai ya mutu, sai kawai ta sunkuyar da kanta tana tunanin abunda zai faru a tsakaninsu idan daran yayi.

Koda ya shiga sashen Uwale domin ya samu Hamra'u da maganar don ya nuna mata kuskuran abinda take a yanzu, ada idan tayi hakan babu laifi amma yanzu tunda yayi aure to abinda yafi kamata ta janye jikinta domin samun zaman lafiya.

Da maganar ya shiga amma abun mamaki sai ya kasa cewa da ita komai gabadaya tausayinta ne ya rufe shi ganin yanda take ta rawar jiki a kanshi, baya tsammanin zai iya watsa mata 'kasa a ido kuma mutukar ya cika shi dan halak ne dole ya aure ta ko dan irin soyayyar da take nuna masa, amma ya tabbatar da cewar hakan ba zata samu ba sai an kai ruwa rana a gidan.

Allah kenan, yayin da ya ci burin angoncewa da amaryarsa a daran ranar sai amaryar tashi ta 'bule jini ya 'balle! godiya tai ga Allah daman tunda ya sheda mata kudirinsa take cikin damuwa ganin wannan jinin ya sanya ta kwantar da hankalinta kamar tsumma a randa.

Da yake ba ta da kirki ba ta fad'a masa halin da take ciki ba ta kyaleshi ya gama sakin jiki domin ba tayi masa waigi da duk sassan jikinta ba pant kawai ta bari a jikinta, ta sakar masa ko'ina yana yin yanda yake so, sosai ita dashi suka kai makura gurin bukatuwa, ya dinga kyarma zufa na keto masa, kaf ya cire kayan baccin dake jikinsa ya raba kafafunsa a kanta kokarin cire pant din yake yaji alamun abu a gurin........Hannu ta rike masa tana girgiza kai, ta d'an ture shi ta tashi zaune tana jan wani irin numfashi gabadaya tsigar jikinta ta tashi.........!

Ya 'kan'kame bayanta yana wani irin nishi! a sar'ke yace." Me yasa zaki min haka? kin san baki da tsarki mai yasa zaki sanya na shagala har na kwadaitawa kaina kasancewa dake uhum! me yasaaa."! ya kare maganar yana fesar da wani irin nishi!!!

Ta dinga jin yanda numfashinsa yake fita da sauri da sauri duk ya rikice mata jikinsa in banda rawa babu abunda yake gabadaya hannuwansa na kan Brest din ta yana wasa dasu......Murya na rawa kamar mai shirin fashewa da kuka yace." Baby please help me! kiyi min wani abu kada ki barni sasakai! zan iya mutuwa babyyyy....! ya k'are maganar yana hura iskar bakinsa cikin kunnuwanta.

Gabad'aya ya gama rikirkita mata lissafi, tausayinsa ne ya rufe ta ta dinga tuna irin yanayin da take shiga idan sha'awa ta kamata, dole ta taimaka masa domin ya samu ya zubar da abunda ke damunsa.

Ta juya tana kallonsa duk ya wani susuce! idonshi ya kada yay jawur!! ya wani 'kura mata ido yana lasar lips d'insa, yanda yanayinsa ya nuna taimakonta kawai yake bukata.

Babu yanda za tayi domin a lokacin wani sonshi da tausayinsa ne ya rufe ta.........Da kanta ta kwantar dashi ya wani kwanta kamar k'aramin yaro.......Hannunshi ya dora saman marar shi yana nuna mata abar tashi da tayi tashin goron zabi, ta mike car! tana harbin iska! "Baby please kiyi min wani abu kinji ko."! muryarsa bata fita yake maganar............Ajiyar zuciya ta sauke a hankali tasa hannunta a kai ta fara ja tana wasa dashi......Wani irin nishi ya fara saki yana sank'amewa a gadon.

Kafin kice kwabo ya rikice! kaf-kaf jikinsa ya dinga yi kamar wanda zazzafan zazzabi ya kama.

Ta cigaba da wasa da abar a hannunta tana kallon yanayin da yake ciki dariya ce take cin ta ganin kamar yana shirin haukacewa sai wani ciccije baki yake......Cikin zuciyarta tace ." Ashe akwai abunda zai rikita guy nan ta'b! ta gano lagonsa.

Rintse ido tayi kafin tasa a baki ta fara sucking ashe abunda yake da farko shafar mai ne!! yanzu ihu!! ya kurma! kamar wanda yake bakin aiki! tai sauri ta cire bakinta tana kallonsa! ya rike kanta yana kokarin mayar wa gurin..............Haka nan ta daure ta cigaba da sucking din shi har Allah yasa ya fara yun'kuri cire bakinta tayi ta mayar da hannunta kai! ya janyota ya matse a jikinsa yana kiran sunan Allah.!

*Allah ya baki Lada ZINATU*

*Duk macan dake kyautata shimfidar mijinta Allah yasa ta cikin aljanna madawwamiya*

*Bana koya iskanci ko lalacewa! buri na a samu zaman lafiya da daidaito a tsakanin ma'aurata*

*Saboda haka ku dauki abunda yake da amfani ko watsar da mara amfani*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Ayi hakuri yau banyi posting akan lokaci ba nayi busy da yawa a min afuwa🙏🏼_

*81&82*
Shi kansa ya san yayi abin kunya dalilin da yasa kenan ya kasa had'a ido da ita, jikinsa a mutukar sanyaye ya lalubi gajaran wandonsa ya lalla'ba yasa, kafin ya sauka daga gadon, kai tsaye bandaki ya nufa yana raya abubuwa da yawa a cikin ransa..........Sai bayan da ya shiga bandakin ta iya dauke idonta daga kanshi kai ta shiga girgizawa tare da mamakin irin abinda ya dinga yi sai kace wani zautacce ko kuma mahaukaci sabon kamu.

Shi din ma tunanin da yake kenan, idan ya tuna abun kunyar da ya tafka sai gabadaya ransa ya b'aci sam bai so hakan ba, domin baya so yarinyar ta raina shi domin ganin girmansa, babu abunda yake bashi haushi da takaici sai in ya tuna ihun! dinga zabgawa! dole yayi ko'karin

kiyayewa anan gaba.

Koda ya fito bai yarda ya kalli in da take ba, jallabiyarsa ya dauka yana sanyawa a jikinsa.......lokacin ita kuma ta tashi ta shiga bandakin domin tsaftace kanta, hakan sai yayi masa dadi yayi gaggawar gama uzurinsa ya nemi guri ya kwanta yana so bacci ya daukeshi kafin ta fito.

Hakan bai samu ba, domin idonsa biyu ta fito duk a kan idonsa ta shirya tana juyowa yayi saurin rufe idonsa fitilar dakin ta kashe kafin taje ta kwanta daf dashi tana kokarin rufe jikinta da bargon dake jikinsa.

Ajiyar zuciya ya sauke lokacin da yaji ta a kusa dashi ya bude ido yana kallonta ta kalleshi tare da kashe masa ido! duk da duhu a dakin yaga irin abunda take masa, gabadaya ta gama kashe masa jiki! sai kawai ya sanya hannuwansa duk biyun ya ratsa kugunta sosai ya manne ta a jikinsa, suka sauke ajiyar zuciya a tare, bakinsa ya dora a saman bakinta kafin yace." Allah yayi miki albarka."

Taji dadin adduar sosai a hankali ta amsa da "ameen" tana kara lafewa a cikin faffadan kirjinsa da take mutukar so da sha'awa.

Bacci mai dadi sukayi wanda suka jima ba suyi irinshi ba, da asubah kusan a tare suka tashi, ya dan shafa gefan fuskarta kafin ya zare jikinsa ya sauka.

Sai da yayi wani wankan sannan ya daura alwala ya fito.

Ya sauya jallabiya da gajeran wando ya shirya tsaf domin shiga massalaci, da casbaha a hannunsa ya tsaya a kanta yana mata magana.

Tashi tayi tana d'an mutsika idanuwanta, yace." Zan shiga massalaci yana da kyau kema tashi kiyi sallah ko."

Ba tace komai ba ta sakko da kafafunta kasa, ganin haka yasa ya kama hanyar fita.

Daurewa tayi ta kori shaid'an din da yake so ya rinbace ta, taje ta dauro alwala ta fito, ta gabatar da sallah bacci yana rinjayarta.

Koda ta idar da sallar gadon ta koma ta kwanta aikuwa bacci mai nauyi ya d'auketa.

Koda ya fito daga massalacin kai tsaye gurin su Uwale ya nufa...........Uwar dakin ya shiga ya sameta kan dadduma da carbi a hannunta,  ya zauna gefanta suna gaisawa da juna.

Tace." Kwana biyu kafafuna duk sun ishe ni da ciwo gashi ina so naje   k'auye bikin 'yar gidan Tasallah makociyar nan tawa ai kasan ma yarinyar Zainabu ita za'ayi wa aure "

Girgiza kansa yayi yana kallonta kafin yace." Baki  da ishashshiyar lafiya Uwale ki zauna a gida ki huta idan na samu hutu zamuje gabadaya."

Tace." A'a ni dai sai naje domin Tasallah ba ta cancanci haka a gurina ba,  ta jima ba tayi sabga ba sai yanzu saboda haka ni dai ka k'yaleni sai naje.'"

Yace." Yaushe ne bikin."?

"Sati biyu masu zuwa."

Yace."To babu damuwa Allah ya kaimu za muje tare  amma ba zamu kwana ba."

Tace."A'a  mu dai zamu kwana gaskiya domin muna buk'atar gaisawa da 'yan uwa mussaman Hamra'u   da ta kwana biyu ba ta ga iyayenta ba."

Shuru kawai yayi yana kallonta ya riga ya san halinta idan ta kafe akan abu shiyasa baya jayayya da ita.

Yana 'kok'arin tashi Hamra'u ta shigo dakin.

Fuska a sake ta tsuguna har kasa tana gaishe shi.

Shima ya saki fuskarsa yana amsawa.

Tace." Yaya na yau irin abincin da kake so nayi mana."

Yace." me kenan."?

Tana 'yar dariya tace." Towon shinkafa miyar agushi."

Shuru yai yana raya wani abu a ransa.

Agogon hannunsa ya duba kafin
Yace."Okey godiya nake kanwata amma ki ajiye min bari naje shirya tukkuna." Ya fadi hakane a zahiri amma a can kasan zuciyarsa ba haka abun yake ba, baya ya san ya gwasale gwanintar da tayi masa, shiyasa yayi mata wannan wayon amma me zai yi da abincinta bayan na amaryarsa yana can yana jiransa, a tunaninsa yanzu gwanar tashi ta kammala masa breakfast tare da ado irin wanda yake bala'in so.

Sai dai me! a kwance ya same ta lakadan tana bacci, ya jima a tsaye a kanta yana kallonta tare da d'umbun mamaki a tare dashi, anya kuwa ma tayi sallah? zuciyarsa ce take raya masa hakan........Ya kalli agogon dake hannunshi bakwai da kwata, kansa kawai ya girgiza zuciyarsa a kuntace! ya fara shirin fita.

Sai da ya kammala tsaf sannan ya tsaya a kanta yana tashin ta.

Ta bude idonta dake cike da bacci! ganinsa cikin inform yasa ta fara kokarin tashi zaune.

Da fuskar bacin rai yake kallonta kafin yace." Wannan shine kuskure mafi muni da za kiyi wanda zai janyo mana samun matsala domin ni ba raggo bane, kuma bana shiri da malalacin mutum shin ina alkawarin da ki ka dauka akaina."

Ta sunkuyar da kanta tana auna maganganunsa! shin wai ita ya za tayi ne? sam bata fahimci abinda yake nufi ba.

Ganin tayi shuru yasa yaja dogon tsaki da fadin." Kin dai yi sallah ko."?

Ta daga masa kai alamun E tayi."

Bai sake magana ba, ya bude drowar gefan gado ya kwashe wasu takardu masu dan yawa ya had'asu tsaf duk tana kallonsa, bai kalli in da take ba ballanatana yayi mata sallama ya sa kai ya fice daga dakin.

Ajiyar zuciya ta sauke bayan fitarsa........Ita fa gaskiya ba ta tsammanin wahalar da kanta akan abunda bata saba dashi ba, domin duk ta fahimci inda maganganunsa suka dosa yana mata shagu'be! da hannunka mai sanda! abunda ta san za ta iya shi kawai za tayi tunda take bata ta'ba dora tukunya da sunan girki ba, to ballanatana har a kai maganar shara da gyaran gado wannan duk hadimanta suke mata, a wannan karon ma abunda ta kudira kenan, babu yanda za'ayi tana da hadimai ta wahalar da kanta.

Kallon gadon tayi duk ya hargitse akwai bukatar ma a sabunta shimfidar gadon.

Girgiza kai tayi tana kokarin sauka daga gadon, tana tunanin kawai zata sanya Baraka ta gyara masa dakin i dan yaso ita Marakisiyya sai tayi masa abinda zai ci, da wannan tunanin ta nufi sashenta .

Da takaici da bacin ranta ya isa gurin aiki.

Tun jiya da daddare rabon shi da abinci, bai ta'ba jin yunwa irin na yau ba, koda yake bai yi mamakin faruwar hakan ba, idan ya tuna irin wahalar da yasha jiya kafin ya samu satisfied ya zubar da sperm mai yawa tun daga lokacin yake jin yunwa, ya dai daure ne kawai har gari ya waye.

Yaji dadin yanda ya samu nutsuwa da ita, amma abunda tayi a yanzu ya 'bata masa rai mutu'ka! sam baya so wani sa'bani mai muni ya shiga tsakaninsu shiyasa yake bin komai a sannu a hankali.

Tsabar yunwar da yake ji ta ha nashi aikata komai, sai kawai ya dauki waya ya kira Hamra'u tare da sheda mata cewa zai turo direba yanzu ta had'a masa abinci.

Cike da annushuwa ta amsa tare dayi masa fatan alkairi."

Ya kashe wayar yana jin wani iri a tare dashi, kwata-kwata bai so hakan ba sai dan babu yanda zai yi.

Baraka ta gurfana a gabanta tare da mika mata key din dake hannunta tace."Ranki ya dade na kammala aikin."

Ta kar'bi key din da fadin." Kin sa turare a dakin ko."?

Tace."Eh nasa ranki ya dade."

Tace."Shikkenan ki tashi kije kawai."

Godiya tai kafin ta tashi ta fita.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta dauki wayarta dake ajiye a gefanta.

Kiran wayarsa tayi, lokacin yana cin abinci yaga kiran nata  kamar  baya so ya daga.............Ta dan sassauta murya da fadin." Ina kwana."

Babu yabo babu fallasa ya amsa. da "Lafiya lau." ta dan ja numfashi kafin tace." Ya aikin ? dama cewa nayi ko zaka turo direba ya daukar maka abinci na kammala." Da karsashi!  da kwarin gwiwa take maganar.

Yana tauna abincin dake bakinsa yace."  lokaci ya k'ure miki  sai da kiyi hakuri domin yanzu haka abinci ne a gabana nake ci  idan kina bukatar naci abincinki sai kiyi himma idan Allah ya kai mu gobe."

Tace." A ina ka samu abinci."?

Kai tsaye yace." Gurin Hamra'u."

Gabanta yayi wani irin faduwa!

Ta maimata maganar.

"Gurin Hamra'u fa kace."?

Yace." Eh kina mamaki ne."?

Wani kuttun takaici ya tokare mata a wuya!!

Kashe wayar kawai tayi wani mugun kishi da b'acin rai! ya turnuke ta.

"Hamra'u! Hamra'u! Hamra'u!!!  wannan yarinya ta zame mata kadangaran bakin tulu!

Ta dinga tunanin irin cin zarafin da za tayi wa yarinyar domin ta huce ba'kin cikin da take kuntuka mata!

Shin wai meye ruwanta da mijinta ne.?

Falo ta fito ta zauna kan kujera kafin ta 'kwalawa Marakisiyya kira.

Da sauri ta fito daga kicin tana amsawa,  tace." Je ki sashen masu gidan kice Hamra'u tazo ina neman ta."

Da sauri ta amsa kafin ta  kama hanyar fita.

Sosai Hamra'un tayi mamakin kiran da take mata, Uwale tace." Ki tashi kije mana kada zuciyarki ta raya miki sharri!

Tace."Uwale bana bukatar wata mu'amula ta shiga tsakanina da matar nan saboda bata da kirki wallahi  albarkacin Yaya na kawai nake saurara mata."

Uwale tai murmushi kafin tace." Kin kyauta ai tashin hankali bashi da amfani ki tashi kije watakila sulhu take nema dake.

Tayi jim tana nazari kafin ta yanke shawarar zuwa.

Ta same hakimce a kan kujera,  sai da taji wani abu ya dan ta'ba zuciyarta, kallon fuskarta tayi suka hada ido, bata hangi komai ba, domin ita gimbiyar ta boye b'acin ranta.

Da hannu ta  nuna mata gurin zama.

A nutse ta zauna kafin  tace." Kin tashi lafiya ."?

Ta amsa da "Lafiya ya kuka tashi? ya Jikin Uwale."?

Tace." Taji sau'ki."

Falon yayi shuru na 'yan mintina kafin tace."Kin san kiran da nake miki kuwa."?

Tace."Aa  sai sheda min."

Murmushi tayi kafin tace." Ni da kaina na ha naki hidima da mijina saboda wasu dalilai na, kiyi hakuri  yanzu na amince miki cewa ki cigaba da ayyukanki nagode sosai wannan shine dalilin kiran, kada kiji komai na yarje miki cigaba da kula da d'an uwanki."

Ba ta kawo komai a ranta ba tace." To shikkenan idan maganar kenan ni zan tafi."

Ba tare da tace komai ba ta nuna mata hanya da  hannu.

Ta tashi ta fita tana jin wani irin dadi domin ita a tunaninta Umar din ne  ya nunawa gimbiyar

muhimmamcinta shiyasa ta nemi sulhu da ita dama ita tasan Umar yana sonta  saboda haka zata sake zage damtse gurin kulawa dashi har tasha gaban duk wata 'ya mace a gurinsa...

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: *LOVE!💔*
*83&84*
Ita kad'ai ta bar wa zuciyarta abinda ta kudurta, malam  ba haushe yace (wanda ya'ki sharar masallaci yayi ta kasuwa) yamma likis ya dawo gidan da tarin gajiya a tattare dashi.

Tsaye ta mike tana masa barka da zuwa.

Tun daga sama har kasa yake kallonta, gabadaya yaji gwiwarsa tayi sanyi yarinyar na da wani irin diri da zubin jiki mai kyau!

Tana sanye da 'kananun kaya wanda suka matse ta riga da wando  tight! hattar da shatin nipples dinta sai da suka fito,  wandon ya manne a jikinta ya fito da sharp din jikinta  wanda yake mutukar  masifar so da 'kwakwa!  sosai  da sosai
Kwalliyar ta tafi da imanin sa.

Ya sauke zazzafar ajiyar zuciya kafin ya janye idonshi daga kanta, ko'karin wuce ta yake, da sauri  taje ta rike hannunshi,   kanta ta d'ora saman kafadarshi.......Be  iya ce mata komai ba kawai yasa hannunshi guda ya rike kwankwasonta a haka suka shiga dakin taba langwabe a jikinsa.

Tare suka zauna bakin gado  ya fara kokarin cire safar kafarsa,  'kasa ta sauka ta kama kafar tana kokarin cire masa.......sai ya mayar da hannushi wuyansa yana cire botiran rigar dake jikinsa, ya ajiye saman gado.

Kallonshi tai  tana dan lumshe idonta.....Yayi saurin janye idonsa daga kanta jin yanayin jikinsa yana sauyawa.

K'afar sa ya dan janye jin kamar tana masa tafiyar tsutsa!

Ta tsurawa yatsun kafar ido gashin da yake kwance kan yatsun take ja a hankali.

Ya sake janye kafar a karo na biyu,  yace." Me ya hakane."?

Murmushi kawai tai kafin  ta koma ta zauna kusa dashi tana nanuk'arsa!

Cikin zuciyarsa yace."kalankasa sai san  jiki da fitinar tsiya!

Hannu ta dora saman kirjinsa tare dan jan nipple dinshi d'aya

Da sauri ya cire hannun  yana d'an harararta, ya riga ya fahimci abunda take so,  kawai sai ya zame kafad'arsa wanda kanta yake kwance ya mike da sauri toilet ya nufa.

Jiki a mace ta dauke kayan da ya cire ta ajiye a in da aka tanada.....gefan bed din ta zauna tare da tsirawa toilet din ido,  wani lokacin har mamakin kanta take ganin yanda ta damu rayuwarta a kansa wai har tana kishinsa, koda wasa ba tayi tunanin hakan na iya faruwa ba.

A gurguje ya fito daga toilet din kasancewar lokacin sallah ya gabato yana kimtsa jikinsa tana aikin kallonsa, kafin tace." Abinci yana jiran ka a daining."

Ya dan juyo yana kallonta kafin yace." Da gaske."?

Kai ta d'aga masa.....'Karamin murmushi yayi kafin yace." Nagode sosai na kuma ji dadin hakan amma sai na fito daga massalaci tukkuna."

Ba tace komai ba ta mike kai tsaye gurin da yake ta nufa.

Yana kokarin fesa turaran ta kar'ba daga hannunsa.

Ya zuba mata gajiyayyun idanuwansa da suke kokarin tona asirin da yake boyewa.

Cikin nutsuwa take fesa masa turaran, shi kuma yana ta aikin kallonta da mamakin abinda take, sam bai tsammaci cewar  hakan zata faru ba, duba da irin rabuwar da sukayi da safe, bayan haka kuma ta kira waya yaki dauka, yayi tunanin daya shigo gidan rigima zata 'balle  sai yaga akasin hakan.

Ta ajiye turaran saman mirror tana kallonsa,  har yanzu idonsa k'uri a kanta da alamar tambaya a tattare dashi.

Karamin yatsanta ta kai saman idonsa, yay saurin motsa kwayar idon kafin ya dawo hankalinsa, tace." Ka tafi massalaci kada ka rasa jam'i ."

Sanyayyar ajiyar zuciya ya sauke kafin ya dauki cazbaha dake saman mirror din, ya kalleta da sakakkiyar fuska "Allah yay miki albarka."

Da farin ciki ta amsa da "Ameen my husband." Murmushi kawai yayi ya juya da niyyar fita.

Ta bishi da kallon so da k'auna tare da ayyana abubuwa masu kyau a tare dashi......Yanda ta daukeshi ba haka yake ba yana da kyawun zuciya.

Sosai yayi mata adduar shiriya da fatan dorewar zaman lafiyarsu,  yanda yake jin ta a cikin ransa yana ganin zai iya kare rayuwarsa tare da ita kad'ai mutukar zata cigaba da kyautata masa tare da bin iyakokin da Allah ya ajiye.

Sai da ya gabatar da isha'i tukkuna ya koma gidan.

Gurin su Uwale ya nufa domin baya tsammanin idan ya shiga sashensa zai sake fitowa yafi bukatar ya zauna tare da gimbiyar tasa yana kallon ado da kwalliyar ta.

Wai akace kowacce mace da irin kissa da kisisinar ta, duk yanda Hamra'u tayi domin ta janye hankalinsa abun ya  gagara! domin dai gabadaya kaf hankalinsa da tunaninsa na kan matarsa magana yake amma tunaninsa na gurin ta.

Tayi- tayi! ta buga dashi kan yaci abinci fafur!  ya'ki, jikinta yayi mugun sanyi dan ba tayi tsammanin faruwar hakan ba, domin tunaninta yana nuna mata cewar sulhu da Gimbiyar ta nema ya samo asali ne ta dalilin jajurcewarsa ashe hasashe kawai take ba haka abun yake ba......Kuka ne kawai ba tayi ba don ganin ha'kanta bai cimma ruwa ba.
Yayi musu sallama ya tafi babu wani 'kulli a zuciyarsa........Ita kam kasa daurewa tayi ta shiga dakinta taci kuka ta koshi!  gaskiya ta gaji da wannan game din dole tasan matsayinta ta gaji da zama ba tare da ta san  meye makomarta..........To itama dai Uwale tunanin da take kenan tana so idan Allah ya kai su 'Kauyen *Kafur!* su samu  zama da iyayen yarinyar domin  su tsayar da magana.

Duk da abincin bai masa yanda yake so ba, haka nan ya daure yaci domin ya 'karfafa mata gwiwa domin duk a tunaninsa itace tayi,   tissue yake kokarin yaga,  ta rigashi  ba jira komai ba ta fara goge masa baki,  fuskarsa a sake yace." Ashe amaryar tawa gwana ce a kowane bangare."

Murmushi kawai tayi ta gyara zamanta kan kujera kamar gaske tace."  Na iya girki ko."?

Yace." Sosai kuwa! yayi dadi amma ko dan gaba ki kiyaye bana san yaji sosai a abinci."

Tace." To zan kiyaye insha Allah."

Shuru gurin ya dauka na 'yan mintina kafin ya kalleta da fadin." Kwana nawa abun yake kafin ya tafi."?

Ta kalleshi da nazarin maganarsa sam bata gane abinda yake nufi ba.

Yace." Ina nufin wannan abun da yayi min karan tsaye ya hana ni amsar hakkina a jiya."

A take ta gane hausar..........Sai kawai ta shagwa'be fuska tana jujjuyawa kwayar idonta a kansa tace." A 'kalla  yana kwana goma ko sati biyu kafin ya d'auke."

Ya d'an harareta da fadin." Ban yarda ba 'karya ne! duk da ban san ya abun yake ba, amma a hasashen da nake kwana uku zuwa shida idan yayi nisa yayi sati, idan ya wuce haka to ya zama lalura."

Tayi shuru kawai tana kallonsa...........Yace." Kin san me."? kai ta girgiza.

Yace." Banyi tsammanin cewa zamu daidaita tsakaninmu da wuri ba, koda yake shi *SO!*   Ya wuce wasa domin duk yanda kake tsammaninsa ya wuce nan."!

'Yar dariya tayi kafin tace." Hakane kam!!

Yace." Ban yarda da ba ina so yau da bakin ki  kice dani Ilove you."!

Cikin wani irin yanayi take kallonsa kafin tace." A'a ni dai sai ka fara fadi tukkuna."

Yace." Jiya bana fad'a miki ba."
Yana nufin lokacin da suke romancing  bai manta yanda ya dinga nanata Ilove you ba adadi ba.

Tace." Ai wannan da dalili,   na yanzu kuwa kana hayyacin ka, sai nafi gamsuwa."

Rikitattun idanuwansa ya zuba mata gabadaya jikinta ya mutu,  tabbas a cikin kwayar idonsa akwai wani sirri wanda yake saurin ladabar da mace.

Cikin wata murya ta mussaman yace." Ilove you *ZINA* i really love you *GIMBIYATA!*  Na baki kaina duka habibty."!

Wani irin hali ta shiga mai wuyar fassaruwa, gabadaya ta rasa yanda za tayi da shau'ki!  ta dago kanta tana kallonsa da gajiyayyun idanuwanta da so ya gamai musu illah tace."  Nima ina *SONKA!* ina da burin kasancewa da kai  har karshen numfashina, amma ina rokon abu daya a gurinka."

Ya d'an had'iye yawun bakinsa da fadin." Ki fada min komeye baki da matsala dani."

Kai tsaye tace." Bana so kai min kishiya."

Yaji maganar kamar saukar aradu a kansa.........Ido ya zuba mata da so ya gazgata maganarta, tabbas har cikin zuciyarta ta fadi maganar.
Baya tsammanin zai mata alkawari domin rayuwar ba a hannunsa take ba, kawai sai yace." Idan kin cika cif  kuma kin cike duk wani gurbi da nake da muradi to ki sanya a ranki cewa ni naki ne ke kad'ai, dan haka kiyi kokarin ganin cika cif-cif  kamar yanda nake bukata."

Ganin tayi shuru tana kallonsa yasa yayi saurin jan kujerar da yake zaune......Kai tsaye gurinta ya nufa ya mikar da ita tsaye, suka kurawa juna ido,  fuskarta ya tallafo cikin tafin hannuwansa kafin ya sanya bakinsa saman goshinta, ta rintse ido ta na jin wani bakon yanayi na ziyartar gangar jikinta......Jiki a mace ta kwanta a jikinsa ya rungumeta tsam-tsam! a haka suka nufi dakin mak'ale da juna.

Romancing din da sukayi yau yafi na jiya domin sun raya daran da wata iriyar soyayya ta mussaman gabadaya ficewa sukayi daga hayaccinsu, mussaman shi da yake kasa sarrafa kansa mutukar yana tare da ita.

Wai akace kowa dai da irin zuciyarsa.............Da sassafe ta tashi cikin k'warewa da iyawa  ta kammala komai, tayi wanka tayi ado sosai duk da zuciyarta a 'kuntace take amma ba tayi zuciya ba,  ta shirya komai cikin kwando mai madaidaicin girma, kai tsaye sashen ta nufa da abincin.

Dai-dai lokacin da suka fito daga wanka a tare, Hamra'u ta fara knocking.

Ta kalleshi da fadin." Mybe Hamra'u ce ka bude mata kofar kawai."

Kallon mamaki yake mata......Tayi murmushi da fadin." Kada ka damu da hakan, ni na umarce ta kan cewa ta cigaba da aikinta, mussaman da safe tunda naga tana da himma!  akan ka fita ba tare da kaci komai ba yasa na yanke wannan shawarar  idan yaso da daddare ni nayi maka abincin.

Bai kawo komai a ran shi ba  yace." Okey tunda kin zabi hakan, to ni a gurina babu matsala." Bugun kofar ya katse maganar  ta,  tace." Bari kawai na bude mata kofar."

Yana kokarin sanya uniform d'insa yace." Okey ba damuwa.........D'aure da 'karamin towel wanda bai gama ratsa jikinta ba ta bud'e kofar gashin kanta jike da ruwa tana gogewa da karamin towel din dake hannunta.

A razane! take kallonta gabad'aya sai jikinta ya fara rawa, wani masifaffan kishi ya tokare mata a wuya.

Murmushi tayi ta kalli tsakiyar idonta kafin tace.'' Shigo mana kin tsaya kina kallona."

Kamar da dutse take magana,  sai da ta sake maimata maganar sannan ta razana! ta kalleta sai kace wata mara gaskiya."

Da hannu ta nuna mata hanya da fadin." Ki shigo Hamra'u."

Ta sauke wata zazzafar ajiyar zuciya gabanta na wani irin fad'uwa!  taja matattun kafafunta ta shiga falon da kwandon abinci a a hannunta sai kace wata house girl.

Ta mayar da kofar ta rufe tana watsawa bayanta kallon banza cikin zuciyarta tace."  'Yar iskar 'karya daga yau idan an ce ki sake shigo min dakin miji  kya 'kara.''

Hamra'u ta tsaya tsakiyar falon sai kace wacce aka dasa ta kasa zama ballanatana ta fara aikin daya kawo ta,  gabadaya ma ta rasa nutsuwarta sakamakon ganin Gimbiyar daure da towel ga gashin kanta a jike da ruwa,  kawai sai taji wasu zafafan hawaye na kokarin kufce mata!

Ta kalleta da fadin." Ogan yana ciki bari ya fito sai ki shiga kiyi ayyukanki.''

Ita dai kasa magana tayi sai aukin kallonta kawai take tana mamakin cika da kasaitar ta, gabadaya k'yashi da  hassada suka rufe mata ido!

Koda ta shiga dakin samun shi tayi  ya gama shiryawa yana kokarin daura agogo a hannunsa, ta kar'ba tana daura masa, yana ta sanya mata albarka........Ba ta fesa masa turare ba sai da suka fito falon,  wanda shi gabadaya ma idonsa ya rufe baya ganin kowa sai ita dake gabansa, dan koda suka fito falon bai ga Hamra'u ba saboda yanda idonsa ya rufe,  tana kokarin fesa masa turare! yana k'o'karin shan bakinta, dan sai tallafo fuskarta yake tana gocewa tare dayi masa dariya.........Kawai sai ya fara kokarin kwance towel din da yake daure a jikinta,  al'amarin da ya sanya Hamra'u suman tsaye!  ta rintse idanuwanta kanta yana juyawa a dakin............Dariyarsu kawai take ji a tsakiyar kanta, kafin taji muryarsa yana fadin." Ba zaki bani na sha ba ko."?

Da sauri ta bude idonta tana kallonsu,  kokawa suke yana jan towel din tana ja tare da kukan shagwab'a!

Hankalinta a masifar tashe! ta dire kwandon abincin dake hannunta ta kama hanya ta fita da mugun sauri kafarta take takawa bata sanin a in da take ajiyewa.

Fitar ta ya sanya ta daidaita hankalinta ta kalleshi duk ya wani rikice tace." Ka bari don Alla jiya fa har gajiya kayi dasha yanzu haka nipples dina zafi suke miki ka bari su warke."

Yace." Ni ban ce miki na gaji ba, kece dai ki ka ha na ni saboda haka yanzu ba zan fita  ba  sai na tsotsa."

Dariya ya bata ganin yanda ya lalace! sai kace soko sai jan towel din yake idonsa yayi jawur!

Tace." Duba bayan ka 'kanwarka tana kallonka."

Yayi saurin juyawa,  hakan ya bata damar rugawa daki da gudu ta murza key tana sauke ajiyar zuciya.

Shima ajiyar zuciyar ya sauke tare da kokarin danne sha'awarsa!  ya kalli kwandon abincin dake ajiye,  falon ya shiga bi da kallo wai  Hamra'un yake nema.

Ganin babu ita a falon ya sanya shi godewa Allah tabbas da anyi abun kunya

A gurguje yayi break fast din kafin ya kama hanyar fita ba tare da ya tunkari inda take ba, domin hakan shine kwanciyar hankalinsa..........

*SAI MUN HADU MONDAY DA IKON ALLAH*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _*Zahirin gaskiya jiya naga sahihin SO!! wallahi naji dadin yanda kuka dinga turareniyar kiran waya ta da masu turo min text messages na fatan alkairi, tabbas adduarku tana tasiri a tattare dani, ba zan gaji da sheda muku cewa nima da bazarku nake taka rawa ba, MANAZARTA abin alfahari na, mutunan kirki ina alfahari daku, ina rokon Allah ya bud'a 'kwakwalwarku ya baku hikima da basirar rubuta abunda za'a amfana dashi, nagode sosai💕 SAI DAKU!✊🏻 MARUBUTA Abokan aiki, baiwa ce ta Allah domin shi ya ajiye hikamarsa a gurin, hannuna yafi karfin rubuta alkairin ku sai dai addu'a da fatan alkairi............NA GAISHE KI (NA'IMA SULAIMAN) (Nimcy luv) matashiyar marubuciya, tabbas al'kalamin ki ba zai ta'ba rubuta shirma ba, saboda aiki da hankali da kuma neman shawarwari, ina miki fatan alkairi tare da cimma burin abinda ki ka sanya a gaba............MASHA ALLAH🙏🏻 Thousands greeting to my fans love you all💕🥰*_

*85&86*
Wannan shine 'karshen matsalar domin ko da wasa Hamra'u bata sake bin hanyar sashen maigidan ba ballantana har ta kai ga shiga dakinsa da wata manufa...........To Sosai suka samu daidato a tsakaninsu suka d'inke kamar tif da taya ke kyace dama can auran so da k'auna sukayi, sun riga sun sabarwa da junansu kwanciya tare cikin bargo daya suyi romancing iyakacin yanda ransu yake so.....sai dai b'angaran sa daurewa kawai yake, domin bukatarsa bawai tana biya duka bane, kawai dai yana rage zafi da hakan, wannan dalilin ya sanya ranar da tayi wankan tsarki kamar ya zuba ruwa a kasa yasha ganin tana sallar asubahi yasa daya dawo daga masjid ya cire jallabiya yayi rashe-rashe a gado yana kallonta tana gyara tarin turarukan dake saman mirror, kallonta kawai yake yana lumshe idonsa tare da shafa kasan mararsa gabadaya a dame yake yanda yake jin jiki baya tsammanin ko yaje gurin aiki zai iya tsinana wani abun azo a gani.

Ta juyo tana kallonsa ganin condition din da yake ciki yasa jikinta ya mutu ita kanta tasan a cikin damuwa yake, kuma ba komai ne ya janyo masa damuwar ba sai tarin sha'awar dake damunsa duk da tana iya bakin kokarinta gurin ganin ta yi masa wasa amma ta fahimci kamar hakan baya gamsar dashi.

A sanyaye ta zauna kusa dashi, ya kama hannunta ya rike yana murzawa......cire hannunta tayi

tare da fadin." Ina kwana."

A kasalance ya amsa yana kokarin janyota jikinsa......Ta matsa a tsorace tana kallon kwayar idonsa wacce ta jirkice tayi jajawur!

"Me kake bukata  wanda za kayi break fast dashi."? wannan tambayar tayi masa babu walwala a tare da ita.

Ya sauke ajiyar zuciya idonshi gabadaya yana kanta yace." Dake nake so na karya kummalo."

Zum'bura bakinta tayi tana dan matsawa daga jikinsa.

Ya bita da wani mayataccan kallo kafin yace." Meye haka kike gudu na ko bakya so mu zama abu d'aya."?

Tsaye ta mi'ke har yanzu taki sakin fuskarta tace." Ni dai ka fada min abinda kake bukata zan shiga cikin gidan yanzu."

Ya mike zaune tare da kokarin janyota jikinsa, ta matsa gefe da sauri.........Yace." Na fada miki ke kad'ai nake buk'ata idan kuma zaki min rowa ne to."

Ba tace komai ba ta kama hanyar fita,  haka kawai taji tana sha'awar taja masa  rai!  haka kawai kai tsaye ba zata bashi kanta ba sai ta wana shi!

Kasa katabus!  yayi  kawai ya saki baki yana kallonta har ta bude kofar dakin ta fita......Sai sanda yaji wani irin motsi da gabansa yayi ya dawo hankalinsa, ya kalli gurin yana girgiza kansa, gabad'aya girmansa ya bayyana bai ta'ba riskar kansa a  irin  wannan yanayin ba.

Lamo ya kwanta yana matse k'afafunsa, ai ko ana ha maza! ha mata! sai ya sake aure saboda irin wannan ranar, domin ya lura mata  da yawa mugwaye ne  basu da tausayi!  amma yana tsammanin ba duka suka taru suka zama daya ba,  yana da tabbacin idan Hamra'u ce ba zata bar shi  cikin halin ni 'yasu ba.

Sosai cikinsa yake ciwo mussaman k'asan mararsa, ga wani irin girma da gabansa ke karawa sai hauhawa yake tamkar ya fasa wandon ya fito.

Kira ne ya shigo wayarsa  dake can nesa dashi.......ya sanya hannu yana lalubanta har Allah ya bashi ikon ganinta.

Asp ne yasan za'a rina wai an saci zanin mahaukaciya.........Cikin sha'kewar murya yake magana.

Cike da kulawa Asp din yace." Subahanallahi baka da lafiya ne."?

Gyaran murya yayi yana janyo maganar da 'kyar yace."  Da sauki dai za'a ace amma ina jin jiki bana tsammanin ma zan fito aiki a halin yanzu."

Yace." Nima abinda nayi tunani kenan, ganin takwas ta wuce baka shigo ba yasa nace lallai akwai matsala, shin me yake damunka."?

Shuru yayi yana nazarin maganar, Asp abokinsa ne kuma  kamar dan uwa yake a gurinsa amma baya tsammanin zai iya fada masa sirrinsa.

Dawurwura! yake domin ya rasa ma abinda zai ce masa.

Yace." Ashe har mun fara haka da kai, ai na d'auka abunda ya shafeka ya shafeni me yasa zaka b'oye min damuwarka? ni fa na d'auke ka tamkar dan uwa na jini."

Gabadaya sai jikinsa yayi sanyi damuwarsa ta sake tsananta Asp din ya gama kashe masa jiki.

Yace." Bafa wani gagarimin abu bane kada ka tashi hankalinka"

Yace." 'Karamin abu ba zai sanya ka damu kanka haka ba, a sanin da nayi maka jarumin namije ne wanda k'aramin abu da babba basa firgita ka babu shakka akwai abunda yake faruwa da kai."

Jin yanda Asp din yake kambaba!  shi ya sanya shi dariya, ya rintse idonsa tare da kokarin danne sha'awar dake damunsa.........Shi kansa mamakin kansa yake, kamar yanda Asp din ya fada k'aramin   abu ko babbah basa ta'ba d'aga masa hankali, amma abun mamaki! abunda bai taka kara ya karya ba shine yake wahalar dashi,  yarinyar ta zame masa matar jaraba ita kadai yake gani a gabansa koda ya hasaso wata macan ba kamar ita ba.

Jin shuru bai magana ba ga wayar na bin iska yasa yace." Kodai har yanzu  ban kai matsayin

da zanji matsalarka ba kayi shuru, bahaushe yace (shuru ma magana ce.")

Ya sauke zazzafar ajiyar zuciya kafin yace." Matsalar mutuniyarka ce."

'Yar dariya yayi domin sai dama ya raya hakan a ransa, shi kansa matsalar da yake fama da ita kenan......Zeey bata barin sa ya sarara, k'orafin yau daban na gobe daban! yafi samun nutsuwa da Madam Uwargidansa, wannan dalilin ya sanya yaji gabadaya auran ya fice masa daga rai yana jin tsoron auro ta ukun tazo ta daga masa hankali domin tun kafin ta shigo gidan tana nuna zafin kishi akan matansa, yasan ba zai samu matsala da Madam ba, Zeey ce 'yar tujara! baya tsammamin kanwarsu zata jiku guri d'aya.

Yana 'yar dariya yace" Umar matsalarka da Zinatu taki 'karewa amma kada kayi mamakin watarana kai da ita zaku iya zama kamar *Laila Majnun!* saboda tsananin so da 'kauna." cikin wasa yake maganar.

Girgiza kansa yayi kafin yace." Bana tsammanin faruwar hakan domin ita wannan yarinyar babu macan da ta kai ta 'keta da mugunta! ban san da hakan ba sai yau."
Iyakar gaskiyarsa yake maganar.

Da sauran dariyar a tare dashi yace." Wai dan Allah me tayi maka ne? nifa kaina ya kulle wallahi."

Tsaki! yaja kafin yace." Rabu da ita kawai ai nima ina da rana."

Yace." Ai tambayar ka nayi amsa ya kamata ka bani naga kana waskewa.

Shuru yayi na second biyu kafin yace." Naga kamar tana jin maganarka kayi mata nasiha cewar abunda take haram! ne mala'iku suna tsine mata! tabbas da taje islamiyya ba za tayi haka ba, amma kai a matsayinka na waliyyin ta sai ka nuna mata hanyar gaskiya."

Shi kam Asp dariya kawai yake 'kya'kyatawa domin ya kamo bakin zaran! *Namiji!* har *Namiji!* mace ta mayar dashi sakarai! koda yake shima hakan take a gurinsa lallabawa kawai yake a gidansa, idan ya fito gurin aiki a fafata!

Yace." Waye ya fad'a maka mata wasa ne! duk isa da jin kai! idan ka shiga hannunsu sai ka raina kanka.......kawai ka iya zama dasu shine samun kwanciyar hankalinka, domin yawancinsu

basu da imani idan wani sa'bani ya shiga Tsakaninku  ta nan suke fanshewa babu ruwansu da dokar Allah! sun bi sun take saboda san zuciya,  amma kuma muma  mazan muna da namu laifin domin bama sanin muhimmamcin matan mu sai bukatar kan mu ta kawo mu, sannan suke da daraja a gurun mu, wannan ba dai-dai bane,  yana da kyau mu gyara kuskuranmu suma matan su gyara nasu."

A sanyaye yace." Kwana biyu zaman lafiya muke sosai kuma na zauna nayi tunani domin gano dalilin da yasa take gudu na ban ga komai ba, kawai dai nafi tunanin mugunta ta shirya min shiyasa ta bari na saki jikina da ita."

Yace." Kasan suna da wani abu, idan kazo biyan bukatarka a gurinsu to burinsu su ja maka rai! yanda na fahimci hakan yana musu dadi."

Yace." Nima nayi tunanin haka mybe tana so naje na fashe mata da kuka ko."?

Asp din ya fashe da dariya  yana girgiza kansa yace." E to hakan ma ba laifi bane zaka iya zuwa amma dai kasan irin kukan da za kayi."

Dogon tsaki yaja kafin yace." Allah ya kiyaye."! da karsashi! da karfin gwiwa!  ya fadi maganar kamar gaske baya kukan😅

Yace." Ka daina cika baki fa."

Cikin jin takaicinsa yace." Ranka ya dade mu bar wannan maganar haka domin wallahi ni raina ne ma yake b'aci!  kawai abunda za kayi anan shine ka kira wayarta kayi mata nasiha watakila taji tausayi na ta bani hakkina, amma ina mai tabbatar maka da cewar idan ta'ki  to zan k'wata ta karfi da yaji."

Yace."Duk ba za'ayi haka ba, kayi hakuri insha Allah zan mata  magana kuma komai zai wuce amma ina so dan Allah ka bata muhimmanci domin su mata babban burinsu suga ana kula dasu gami da nuna musu soyayya."

Murmushi kawai yayi yana girgiza kansa, a ganinsa duk wata kulawa da soyayya ya bawa yarinyar kawai dai ta shirya zalinci ne don ganin ya jarabtu da tsananin sonta.

To kamar yanda Asp din yayi alkawari zai kira wayarta domin yay mata nasiha hakane ya faru..........bai fito 'karara ya nuna mata abunda yake nufi ba, amma yayi mata hannunka mai sanda wanda yasa ta fahimci abunda yake nufi.......Ba ta iya cewa komai ba, har yayi mata sallama,  ta kashe wayar tana sauke ajiyar zuciya.

Tabbas bata raba daya biyu shine ya shedawa Asp din abunda yake faruwa a tsakaninsu..............Ita fa akwai manufarta kai tsaye  ba zata amince masa ba a yanzu sai nan da wasu kwanaki.

Na farko tana tsoron daukar ciki  tunda tsarkinta  kenan.........tana da tabbacin cewa idan rabo ya rantse  a tsakaninsu za ta iya samun ciki dalilin k'ofofin jikinta da suke a bude.....Wannan shine babban dalilin da yasa take gudunsa, tafiso ko wani abu zai  shiga tsakaninsu  ba yanzu ba tukkuna.

Wanka tayi taci gayu tana kamshi turare kala-kala ta zauna a falo tana kallo tana tsikarar duniyarta da tsinke babu abunda ya dameta!

Ta manta dashi domin duk a tunaninta ya tafi gurin aiki.............Kawai sai ta tura Baraka ta nufi sashen domin gyarawa kamar koda yaushe.

Baraka tasa key tana muzara kofar taki bud'ewa,  shi da yake kwance a uwar daki ya dinga jin motsi ya fito falon yana tambayar waye."

Gabanta na faduwa tayi saurin barin gurin.........tana kokarin shiga wani korido ya hango bayanta, nan ya fahimci cewa d'aya daga cikin masu aikinta ne, ya koma ciki da mamakin hakan a tare dashi.

Baraka ta sheda mata cewar yana nan bai fita ba,  jikinta a sanyaye tace." Amma dai  baku had'u ba ko."?

Da sauri tace." Eh ai jin yay magana yasa da sauri  na matsa daga gurun.

Ajiyar zuciya ta sauke tare da jin sanyi a cikin zuciyarta, tasan duk ranar da yasan abunda yake rufe akwai rikici.

Sai bayan la'asar ya samu kansa,  a gida ya gabatarsa da sallah dan bai iya shiga massalaci ba gudun abunda ka iya zuwa ya dawo kawai ya hakura yayi sallar a gida...............Kai tsaye

sashen Uwale ya nufa  ya same su zaune a falo suna kallo.

Ya samu guri ya zauna yana kiran sunan Allah.....Uwale ta kalleshi da fadin." Ashe baka fita."?

Yace." Eh wallahi na yini bana jin dadi sai yanzu na samu sassauci."

Tace." Ayya ai ba labari me yake damunka."?

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Ciwon ciki ne amma yanzu da sauki tunda nasha magani."

Tace." To Allah ya sawwake." Ya amsa da "ameen yana kallon gefan da Hamra'u take zaune sai cika take tana batsewa!

Abun ya bashi mamaki sosai!  yarinyar ba ta'ba share shi irin yau ba......Cikin kulawa yace." Kanwata lafiyarki kalau kuwa? bako gaisuwa."

Ta kalleshi tana sake hasaso abunda ya faru! kawai sai wasu zafafan hawaye suka ciko idonta.......Wani irin haushinsa take ji tare da masifar kishin matarsa.

Sunkuyar da kanta tayi tana kokarin boye hawayen kada ya zuba.

Uwale tace." Ai Hamra'u kwana biyu ta zama shuru-shuru! ko ni ma da kyar take min magana."

Da kulawa yace." Ko baki da lafiya ne."?

Kai ta girgiza kuka naso ya k'wace mata.

Yace." To ki daina damuwa komai yana da lokaci dan haka ki kwantar da hankalinki."

Wannan maganar da yayi  ta sanyaya mata zuciya......Ta kalleshi tare da sake jin sabon sonsa na ratsa cikin jikinta......Murmushi yayi mata da fadin ." Ko zaki iya taimaka min da abinci."

Tai murmushi da fadin." Me zai hana bari na kawo maka."

Ta ajiye romot din hannunta ta nufi kicin tana adduar samun nasara a zuciyarta.

Ido ya dauke daga kanta shima adduar yake a cikin zuciyarsa Allah ya bashi ikon yi mata adalci.

Uwale ta kalleshi da fadin." Ina matar taka ina fata dai lafiya lau kuke zaune."?

Yace." Lafiya lau ai tana zuwa ku gaisa ko."?

Girgiza kai tayi da fadin." Oho! o! ni ai na kwana biyu rabon dana sa ta a idona."

Da mamaki a tare dashi yace." Kina nufin bata zuwa ta gaishe ki "?

Yanda ya fadi maganar a harzuke!  yasa jikinta yayi sanyi ta dinga nadamar subtar bakin da tayi, kwata-kwata bata so wani sa'bani ya shiga tsakaninsa da matarsa

Ganin tayi shuru yasa ya gazgata maganarta, ransa ya 'baci mutuka, ashe duk zaman da suke a gidan ba ta zuwa ta gaishe da kakarsa wannan wane irin raini ne."?

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanku. bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  4k  kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin

ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukan ki ya 'kare da ikon Allah._

*87&88*
Ta kalleshi da fadin." Aa' Umaru naga kamar ka fusata! ban fada maka maganar nan da wata manufa ba, don Allah kada aikata abinda ba shikkenan ba, domin na san ka da fushi! kada kaje ka haikewa 'yar mutane akan abunda bai zama dole ba."

Yace." Dole ne tazo ta gaisheki dan ba zan lamunci wannan rashin arzkin ki ba, tsayin kwanakin da tayi a gidan nan me yasa baki fada min abinda yake faruwa ba sai dana tambaya sannan, Uwale kina da mutukar muhimmanci a gareni saboda haka duk wanda nake ta tare dashi ya zama lallai ya daraja ki ya mutuntaki."

Jikinta a mace tace." Nasan da haka Umar domin ba tun yau ba na sheda cewa kana da kishin kanka da kuma magabatanka, amma yana da kyau kafin ka yanke hukunci kayi tunani tukkuna, ka duba irin da'bi'un yarinyar sannan kai mata uzuri don Allah kada ka tsawwala mata cikin ruwan sanyi nasiha take ratsa jikin mutum, amma na tabbatar da cewar idan kaje mata da hayaniya to za'a samu matsala abunda bana bukata kenan."

Ganin yanda duk ta tashi hankalinta yasa jikinsa yayi sanyi, tuntuni Asp ya sheda masa hakan, cewa yawan tsawa! ko hargagi basa shirya mutum nasiha da janyo mutum ajiki shine abinda ya dace.

Hamra'u dake zuba masa abinci sam! ba taso hakan ba, yanda taga ya fusata! taso ace Uwale ta bari yaje yaci mutuncin matarsa shiyasa gabadaya haushin Uwale ya tu'keta, tana gama zuba masa abincin ta shige dakinta ta zauna tana tunanin mafita, a duniya idan akwai wacce ta tsana to ZINATU ce domin itace tayi mata karan tsaye gurin tabbatuwar burin dake ranta.

Hira sukayi sosai da Uwale irin wacce suka jima ba suyi irinta ba, dalilin rashin samun lokacisa..........Wannan damar ta samu ta sheda masa irin hukuncin da ta yanke domin ita kanta al'amarin ya isheta Hamra'u tana yi mata wani irin kallon zargin a ganinta kamar Itace bata da goyon bayan ya aureta ba.

Yace." Shikkenan kada ki damu idan Allah ya kaimu k'auyen Kawu Ado zai samu mahaifinta su tattaunar maganar insha Allah."

Tace." Yawwa har naji dadi a raina, a kalla dai ko kudin zance aka kai musu kaga ai hankalinsu

zai kwanta, amma kaf garin ya dauka cewa saboda kayi kudi ka zama wani abu a duniya shiyasa kaqi auranta, da yawa mutane zargin da suke kenan, amma yanzu duk wanda yaga an kai kudin zance zai cire shakku a kan al'amarin.

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Uwale al'amarin mutane yana da wuyar sha'ani, ni duk wannan maganganun basa damuna domin nasan rayuwata ba a hannuna take ba, duk yanda naso da na tafi da ita idan Allah bai so hakan ba to babu yanda zanyi, wallahi a tarihin rayuwata ban ta'ba tunanin wai zan zama ma'aikacin gwamnati ba, ballanatana har na samu wani babban matsayi wanda duniya tasan ni dashi, sannan kuma ban ta'ba tunanin wai zan auri 'yar sarauta ba, wannan yana d'aya daga cikin hukuncin ubangiji, yana kuma da kyau mutane su gane cewa rayuwar duk da suke takaitacciya ce, domin Allah kan iya juya al'amari a kowanne lokaci.

Uwale ta girgiza kanta da fad'in." 'Kwarai Umaru zantukan ka duk gaskiya ne, duniya a fai-fai take juyawa take na kasa ya koma sama, kana kuma wanda yake sama ya dawo kasa, mai imani da tsarkin zuciya ne zai yarda da kudurar ubangiji.

Kiran sallar magriba ne ya katse tattaunawar da suke, da sauri ya mike yana kallon agogon dake daure a hannunsa, yace." Zan shiga massalaci yanzu watakila na dawo, idan kuma kun ji shuru sai da safe insha Allah."

Tana kokarin tashi tace." To shikkenan babu damuwa Allah ya bamu a ran rai da rayuwa."

Ya amsa da "ameen." tare da kama hanyar fita..........Kai tsaye massalaci ya wuce a can yake tunanin daura alwala.

Tun bayan fitowarsu daga massalacin suke tare har misalin takwas da rabi, maganar dai suke sake tattaunawa......Asp din na sake bashi shawarwarin yanda zai zauna da iyalinsa lafiya, dole sai anyi hakuri tare da kawar da kai sannan za'a samu zaman lafiya, yace masa lallai sai yayi hakuri ya kawar da kai sannan komai zai daidaita. amma kuma yayi k'okarin ganin sun zama abu daya dashi da matarsa hakan zai taka muhimmiyar rawa gurin daidaituwar al'amarin gabadaya.

Da wannan tunanin ya shiga gidan, bai tunkareta ba tukkuna sai da ya shirya kansa sannan yayi wanka ya sanya kayan bacci masu taushi sai wani irin 'kamshin turare yake mai dadin gaske.

Fitowarta kenan daga wanka ya shigo da sallama a bakinsa........amsawa tayi tare da dan tsayawa tana kallonsa.

Shima kallonta yake tsigar jikinsa na wani irin tashi,  a kasalance ya janye idonsa daga kanta ya nemi gefan gado ya zauna.

'Karamar ajiyar zuciya ta sauke taje ta zaune kurjerar mudubi tana tsane jikinta da karamin towel.

Ido ya tsirawa fatar bayanta kamar yaje ya rungumeta haka yake ji sai dai ya daure a hankali ya kirayi sunanta.

Ta amsa tare da juyowa har yanzu taki sakin fuskarta.

Yace." Ni dake mun zama kamar b'akin juna wai me yake faruwa ne."?

Uffan ba tace masa ba kawai ta  d'auke kanta tana me cigaba da shafa mai a fatar jikinta.

Ya iske inda take bai jira komai ba ya zuba dukkan hannuwansa a saman kafad'arta hannayen suka sauko  saman breast d'inta......Da sauri ta cire hannun, ya sake mayar wa gurun yana kokarin kwance towel din.

Cikin shagwaba tace." Ka bari dan Allah."

Yanayin maganarta ya kwaikwaya ya mayar mata da amsa kamar haka.

"Um-um!! ni bazan bari ba sai kin fada min abinda yasa kike gudu na."

Yanda yayi maganar yayi  masifar jefata cikin wani yanayi gabad'aya jikinta ya mutu wani irin feeling ya dinga damunta.

Jin tayi shuru ba tace komai ba yasa ya dan sunkuyar da kansa yana lasar fatar jikinta mussaman wuyanta lasa yake kamar wani maye.

Ta dinga ture fuskarsa yana sake mayarwa......Kuka tasa tana buga kafa da fadin." Ka daina bana so."

Ya sake  tuburewa!  ya zama kamar mahaukaci sabon kamu!  yana bala'in son shagwabar da take masa.

Kunnanta d'aya ya shiga tsotsa, kafafunta suka dinga kyarma! saura kadan ta rikito daga kan kujerar da take zaune....Ya tallafe ta  sai kokarin rungumeta yake  tayi namijin kokarin fizge jikinta.

Ya bita da wani irin kallo jikinsa duk a mace.

Itama jikin nata duk ya mutu dan kasa aiwatar da komai tayi kawai ta zauna gefan gado tana mayar da numfashi.

Nutsuwarsa ya shiga kafin ya kalleta babu wasa a maganarsa yace." Kiyi alwala zamu gabatar da sallah irin ta ma'aurata."

Gabanta ya buga,  tace." Ai ni nayi sallah ta .'

Yace." Wannan ta daban ce tana da mutu'kar amfani Annabi ne yayi kuma ya umarce mu da aikata sunnah ce mai karfi."

Shuru tayi tana kallonsa........Ya sake shan kunu da fadin." Naga alamar zaki bani wuya to kisa a ranki cewa yau din nan zamu zama abu daya.

Miyau! ta hadiya da kyar tace." Ban gane nufin ka ba nifa ban shirya komai ba, kuma ka daina gaggawa dan jinin har yanzu bai  tafi ba."

Ya kai minti uku yana kallonta kafin ya girgiza kansa da fadin." Kinga bana san doguwar magana za kiyi abunda nace ko kuma sai na shedawa mahaifinki ai ina da number wayar sa yanzu zan kira shi na sheda masa cewa yau tsayin sati biyar kenan baki bani hakkina na aure ba.

Yanda ya fadi maganar cikin rashin wasa yasa jikinta ya mutu.............Ta kalleshi taga yana lalube a wayarsa, da sauri ta fizge wayar ta jefa saman gado. toilet ta nufa tana zumb'ura baki itafa gabadaya ba ta shirya faruwar hakan ba.

Sallah sukayi raka biyu irin ta sabbin ma'aurata,  ya jima hannunsa a saman kanta yana ta

zabga addua, har ta dinga mamakinsa ashe yana da ilimin addini haka.

Tambayoyi ya shiga yi mata akan addini ta bashi amsar wanda ta sani wanda ba ta sani ba kuwa shuru take

Nan ya fahimci cewa lallai tana bukatar karin sanin ilimin addini domin yana bukatar yaga ta zama cikakkiyar mace.....Wato *Mar'atussaliha* wacce zata tarbiyan tar masa da 'ya'yan da zasu haifa.

Tana zaune a saman daddumar ya tashi yaje ya kashe fitila dakin yayi duhu.

Ganin haka yasa da sauri ta tashi taje ta 'buya bayan labule..

Inda yake tsammanin samunta ya nufa yana lalube da hannunsa, babu ita babu dalilinta............Da sauri yaje ya kunna fitilar haske ya gauraye dakin, idonsa yake rarrabawa a dakin bai gano ta ba.

Yana kokarin bude kofar fita ya hango kafafunta a kasan labule.

Girgiza kansa yayi cikin takaici ya nufe ta........Ganin zuwansa yasa tayi wuf ta fito zata gudu! hannunta ya dam'ke! ya rike da kyau! yace." Me yasa kike abu kamar yar k'auye wannan ai gidadanci ne sam ban tsammaci haka daga gurinki ba."

Tana turjewa a gurin, tace." To ni ban shirya ba ka kyale ni mana."

Ya girgiza kansa da fadin." Baki isa ba babu ruwana da shirin ki ai na ma yi kokari yau satin ki biyar a gidanan ban yi komai ba ai a jinjina min."

Ta fara 'kananun maganganu! da buge-buge! hannu yasa ya rufe mata baki hasken dakin kawai ya kashe.....................Labari ya sauya, dan duk turje-turjen da take da nuna rashin yarda yana dora mata nauyinsa ta saduda! har ta fishi kid'imewa! domin ya gama gane lagonta shiyasa ta shiga hannunsa, ya dinga sarrafa ta iya san ransa, tana wata irin shashsheka kamar mai shirin fashewa da kuka........Duk da a d'okance yake bai yarda ya shegeta ba sai da ya

tabbatar da cewa ya gama kai ta k'arshe  sai ya kirayi sunan Allah kafin ya karanci adduar saduwa da iyali  ya fara kokarin shiga gurin da yake kulafuci da 'kwa'kwa!

Ba tayi buge-buge ba!  tsai!  ta tsaya tana jin irin d'auki ba dadin da yake a gurin,  a jikinta take jin yanda jikinsa ke wani irin rawa, sai kokawa yake da abar tashi taki shiga kamar ma ta girmi gurin da kyar da jibin goshi rabi ya shiga...........Lokacin ta galabaita mutuka domin gurin gabadaya ya rikice mata da wani irin radadi da zugi! mara fasali!

Ta d'an daga kafafunta hakan ya 'kara gigitashi!  ya cigaba da cucuku! yana furzar da wani irin huci!

 Murya a dashe!  tace." Idan ba zai yuwu ba kawai ka hakura ni kam na gaji wallahi."!

A rikice!  yace." Zai yuwu kedai ki cigaba da  taimaka min kinji ko amma kuma me ya janyo hakan bayan da ni'ima ta tattare dake."?

Shuru tayi masa domin ita ba ta san amsar da zata bashi ba, kuma ba ta san wane irin taimako za tayi masa ba.

Kamar zai fashe da kuka ya gyara gwiwowinsa yana ta zufa! tare da cizan lips d'insa, ya cigaba da kokarin ganin ya wuce gurin, domin shi kansa ya daddauje ballanatana ita.

*Wai wuya makarantar kare!* duk jarumtarsa da k'yar ya iya wuce gurun, domin wani irin sakarai ya zama ya rasa ma yanda zai yi, koda yake akwai rashin sabo.............Sosai suka ji jiki ita dashi, amma ita tafi shi galabaita dan shi yana wuce gurin wahalarsa ta 'kare mussaman da yaji shi cikin wani irin guri mai taushi cike dam-dam! ruwan ni'ima  na gudana! ai sai ya kwarkwarce!  ya dinga bugunta yana buga sambatu, bakinsa yaki rufuwa! koda yake sunan Allah yake kira yana kuma sanya mata albarka wacce bata da dadi.

Wannan daran ya zama na tarihi a gurinsu domin a cikinsa suka zama abu d'aya! kuma a daran Allah ya saukar da ikonsa domin buwayarsa ta wuce haka....

*_ALLAH YA BADA ZURI'A MASU ALBARKA_*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*

*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 4k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*89&90*
Da k'yar ya iya raba jikinsa da nata. Gabad'aya jikinsa ciwo yake masa mussaman tsakanin cinyarsa da gwiwowinsa.....hannu yasa yana laluben gadon. kawai yaji ya sauke hannun kan Brest d'inta, da sauri ta cire hannun nasa ta jefar dashi tana me cigaba da shashshekar kukan da yake jinsa har cikin zuciyarsa.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke ya yun'kura ya sauka daga gadon ba tare da ya dauki gajeran wandon nashi ba, kai tsaye toilet ya nufa yana had'a hanya kamar wani d'an magyaru!

Ita kam bedshirt din ta cikwikwiye tana wani irin kuka kamar wacce aka aiko mata da mutuwar iyayenta.

Haka kawai take jin kamar wani abu zai faru anan gaba, gashi ya cuce ta ya raba ta da budurcinta.

Haka ya fito daga toilet din ya sameta sai kuka take.

Babu kuzari a tattare dashi ya shirya jikinsa kafin ya cimma in da take kwance.

Cikin sassauta murya ya kira sunanta....*"ZINA."* sautari da haka yake kiran ta.

Tana jinsa tayi masa shuru bala'in haushinsa takeji.

Ya sake kiran sunanta da fadin." Kiyi hakuri kada kisa damuwa a ranki wannan abu da ya faru tsakaninmu alkairi ne ni nayi miki alkawarin rike miki kaina ni naki ne har abadah."

Maganarsa ta d'auki hankalinta ta yun'kura da kyar! ta tashi zaune tana kallonsa,  yana tsaye a kanta sai kace wani mummuni! sai karyar da kansa yake.

Kukan da taci ya sanya muryarta bata fita sosai tace."  Ka cuce ni ka raba ni da budurci na bayan ban shirya hakan ba, haka kawai nake ji a jikina kamar akwai abunda zai faru anan gaba na fada maka bana san kishiya bana shiri da ita."! ta karasa maganar da shashshekar kuka a muryarta.

Gabansa na faduwa! kadan yace." Idan wannan ne matsalarki to ina so yanzu ki sa a ranki cewa ke kad'ai ce uwar 'ya'ya na  dake  kadai zan rayu  ai na samu abu mai muhimmanci a tare dake dole na daraja ki na mutuntaki!  kada ki damu ni UMARU naki ne ke kad'ai ki rubuta ki ajiye wannan."

Ta dinga kallonsa tana so ta gazgata maganarsa.......Ganin haka yasa yayi amfani da damar sa, ya dinga narkar mata da k'wayar idonsa yana karyar da kai da murya tare da shirya mata dadin baki irin na yaudara!  *(mayaudaran maza sun ma fi yawa a cikin maza dayawa sune suke haddasa fitina da tashin hankali a gidansu.......mu kuma mata da tausayi da saurin mi'ka wuya namiji na zuwa da 'yar murya sai mu saduda mu yarda da dadin bakinsu,  to bari kiji har ki mutu ba zai ki daina d'aukar darasi akan namiji ba🤭 ALLAH ka bar mu dasu, ka shirya mana su,  ka basu ikon fad'in  gaskiya ka kuma basu ikon adalci)*

Ya gama kashe mata jiki  da  mayaudarar kalamansa  zuciyarta tayi sanyi ba tayi wani dogon nazari ba ta amince da kalamansa...........*(Kada soyayya tasa mijinki yayi miki dadin baki kan cewa shi dake kad'ai zai rayu, 'karya yake!  domin wallahi zuciyarsu a haka take  haka  Allah ya hallicesu  da son mata,  zakiga namiji da mace hudu a gidansa duk mallakinsa amma ba zaki rabashi da wasu a waje ba............shakulatun 'bangaro zakiyi dashi a duk sanda yazo yana miki wannan manganganu, idan kuwa ki ka yarda da labarin k'anzan kurege!  to kina ruwa😅 In ji (HAMISU BREAKAR) sai dai kiji ana ayyyyyiririiiiii!*

Soyayya suka dinga bugawa! irin wacce  take bala'in so da kwakwa! dan idan wani sa'in ta rike wuta har makara yake a gurin aiki,  Asp yay ta tsokanarsa, shi kam murmushi kawai yake daga zarar kuwa  ya samu sauk'in aiki  zai kira wayarta suyi ta jifan junansu da zafafan kalaman soyayya.

Hamra'u tsantsar tashin hankali da damuwa ta shiga dan ganin yanda mutumin nata ya ajiyeta a gefe.........Da farko ta d'auka matsala ce zata afku, tun bayan da Uwale ta sheda masa abun da yake faruwa.

Amma abun mamaki sai taga a washe garin ranar be ma fita aiki ba, yana tare da matarsa tun safe bai shigo in da suke ba, saboda tsabar bin diddigin da take masa har fita tayi ta tambayi direbansa cewar ya fito daga gidan ko kuma yana ciki.

Budar bakin direban yace." Ai Oga yau ba zai fita ba domin tun safe ya kira ni yake sheda min hakan.

Jikinta a sanyaye ta koma gidan........koda ta gifta sashen sai taji a zuciyarta kamar ta shiga domin ganin abunda ya ha nashi fita.

Da 'kyar! ta iya kai kanta dakinta, tayi kwance a saman gado tare da tsirawa rufin dakin ido......zafafan hawaye ne suka shiga tsere a saman fuskarta.

Can yamma! taji maganganu a falo...ta d'auka baki sukayi koda ta fito........Sai kawai tayi tozali dasu, suna zaune kujera daya sunci uwar kwalliya mussaman ita Gimbiyar kamshin turaransu duk ya cika gurin.

A take gwiwarta tayi sanyi kafafunta suka dinga wani irin rawa, bango (garu) ta dafa jin tana neman zubewa a gurin.

Babu yabo babu fallasa yace." Kanwata kin fito."?

Kallonsa tayi tana danne kukan dake kokarin kufce mata, wai shin ita ya za tayi da wannan kaddarar....Mutumin data ci wahala a kansa ta b'ata lokacinta a kansa shine yake rayuwar aure da wata akan idonta...........Kanta ya dinga juyawa! take ta zube a gurin bata san in da kanta yake ba.

Gigicewa sukayi gabadayansu mussaman shi ya kai ya kawo a gurin hankalinsa ya tashi ainun! bai san lokacin daya dauketa ba ya fita da ita Uwale ta rufa masa baya tana gyara yafan mayafinta.

Tsayuwa kawai tayi a gurin tana mamakin abinda yayi.

Yarinya baliga kuma ba muharramarsa ba ya wani dauketa har da mannata a kirjinsa........Takaici da bakin ciki kamar su kasheta,  tayi kwafa tare da girgiza kanta,  sashenta ta nufa tana tunanin irin hukuncin da za tayi masa idan ya dawo domin ita ba zata yarda da wannan iskancin ba.

Abin mamaki! jininta ne ya hau sosai! lokacin da likita ke sheda musu hakan, abun sai ya basu mamaki!  shin wane irin tunani yarinyar ta sa a ranta haka wanda har zai janyo mata hawan jini.....Ita dai Uwale ta zargi wani abu, shine dai har yanzu beyi hasashen cewa rashin adalcinsa ne ya janyo mata kamuwa da lalura ba.

Da kanshi ya bukaci cewar ta kwanta a asibitin zuwa gobe domin  ta sake samun sauki sosai, domin a zahirin gaskiya hankalinsa ya tashi da al'amarin, yana tsoron kada yar mutane ta had'u da lalura a hannunsa.

Sai bayan isha'i ya bar asibitin.........Yana shiga barrack din Asp ya fito daga block d'insa da waya a kunnansa.

Motar ya tsayar ya sauke gilashi yana kallonsa har ya k'are wayar  ya mayar da ita aljuhu ya k'araso bakin motar .

Hannu ya mi'ka masa suka gaisa kafin yace." Yanzu mutuniyar ta shiga gida ai ta jima a gurinmu kasan Zeey mutuniyarta ce."

Yay jim yana kallonsa da nazarin maganarsa.

Shima Asp din ya fahimci wani abu, sai jikinsa yayi sanyi   yace." Akwai magana kenan dan naga kayi sak! kodai bata fada maka ba."?

Bagarar da maganar yayi kafin yace." Ina cikin damuwa wallahi yarinyar nan Hamra'u ce take kwance a asibiti babu lafiya."

Da sauri yace." Subahanallahi me yake damunta."?

Ajiyar zuciya ya sauke kafin ya furzar da wani irin huci daga bakinsa yace." Haka kawai ta yanke jiki ta fadi  yanzu likita yake tabbatar min da cewa jininta ne ya hau."

Asp din ya jima yana kiran sunan Allah da jimanta al'amarin.....Yace." Jininta ne ya hau akan

wane dalili kodai tana da damuwa ne."?

Yayi shuru yana nazarin abinda kwakwalwarsa ke tuna masa tunda ya fito daga asibitin yake nazari da tunani.

Yace." Baya rasa nasaba da mu'amula ta da matata kasan mata da kishi dasa abu a rai mybe wannan ne ya janyo mata matsala.

Ya kalleshi da fadin." Hakane yanzu kai wane hukunci ka yanke? a zahirin gaskiya idan ba kayi wani abu ba akan yarinyar nan ba to hakkinta yana iya kama ka da kowane lokaci saboda haka ka zauna kayi nazari da tunani a yanda kake bani labarin hallacin da tayi maka yaci ace kayi wani abu wanda zai nuna mata cewa lallai kana da niyyar auranta."

Murmushin takaici yayi kafin yace." Wallahi gabadaya kaina ya kulle Asp na shiga rud'u! ina jin tsoran auran yarinyar azo ana tashin hankali abunda bana bukata kenan bana son matsala ko yaya take.

Ya dinga kallonsa yana girgiza kai kafin yace." Ka zama namiji mana abokina rigima kake gudu to bari kaji da kayi aure da ba kayi ba, kullum a cikinta kake, domin ba zata daina zarginka ba, gwara ma kayi da hujja! amma ban ta'ba tunanin cewa Zinatu zata dinga baka tsoro ba a yanda na sanka haba *Jan wuya!* kada ka bani kunya mana."

Dariya kawai yayi yana girgixa kansa, lallai akwai rikici a gabansa dan wallahi idan ya tuna Gimbiyar tashi gabansa har wani faduwa yake.

Sallama sukayi da juna yaja motar ya bar shi a gurin yana daga masa hannu.

Yana shiga dakin kafarsa ta cake! da kwalba! duk da a cikin takalmi take sai da yaji rauni jini ya fara zuba ya rike kafar yana d'ingisawa, gefe guda ya matsa yana bin dakin da kallo.

Komai a hargitse duk ta farfasa masa manyan turarunkansa masu tsada! kayansa muhimmai ta watsar dasu a kasa, dakin dai tamkar anyi yak'i a ciki!

Kafin ma yayi wani yunk'uri ta turo kofar dakin ta shigo........Kallo daya yay mata ya hango tsantsar tashin hankali a tattare da ita.

Jarumta! ya aro! yayi bala'in shan kunu! da fadin." Meye  haka! waye yayi min kaca-kaca da daki."?

Ta nuna kirjinta da hannu " Nice nan."! da karsashi da kwarin gwiwa ta fadi maganar!

Yace." Kece akan wane dalili? ko kina hauka ne."?

Wani b'acin ran ya sake turnuke ta! tace." Kaine mahaukaci butulu maci aman...........Ya wanke fuskarta da lafiyayyan mari!  yana wani irin tsuma!  ya nuna kansa da fadin." Ni kike zagi saboda baki da mutunci."?

Hawaye na zuba share-share a saman fuskarta........Tace." Kai waye da ba za'a zage ka ba maha'inci kawai."!

Ya sake fusata! amma beyi yun'kurin dukanta ba saboda baya so ya saba da hakan  ya danne bacin ransa yace." Ki fada min abunda nai miki wanda ya janyo har kike kira na da sunaye masara ma'ana."

Taja hanci  tana shashshekar kuka tace."  Ba ni da lokacin zama na fada maka abunda kayi ai kai mai hankali ne ka zauna kayi nazari da tunani mtssswww!."  ta k'are maganar da dogon tsaki!  kafin ta juya ta fita zuciyarta kamar ta fashe saboda bacin rai!

Da d'ingishi  ya fita domin kwalbar ta cake shi sosai!  d'aya daga cikin hadimanta maza ya kirayi d'aya  shi ya jagoranceshi  har cikin dakin ya bashi umarnin cewa ya gyara masa,  ya zauna kujerar falo yana duba kafarsa, dole sai anyi dressing din gurin domin duk  da ya cire kwalbar gurin yana bukatar gyara.

Da yake a barrack din suna da likitocin dake duba lafiyarsu sai kawai ya kira daya daga cikinsu yazo ya dubashi ya bashi maganin rage zugi.

Allah yasa ya gabatar da sallolinsa, kawai sai ya kwanta saman kujera yana mayar da numfashi..........Ya riga ya gano dalilin da ya sanya ta aikata wannan haukan! bai san wane irin kishi ne da ita ba.....hakika auranta yana nema ya zame masa matsala. shi kuma irin tashi jarrabawar kenan.

Washe gari da ciwon jiki ya tashi domin k'afar ta tashi ta kumbura! haka nan ya daure yayi

shirin fita domin baya tsammanin zai iya zaman gidan saboda gudun tashin hankali.

Bai fita ba sai da ya nemi inda take saboda baya so ko yaya Allah ya tuhumeshi da hakkinta.

Tamkar bata da damuwa haka ya sameta ta cakare! tayi gayu na kere sa'a! jikinta da dakinta in banda kamshin turare babu abunda yake.......Cikin zuciyarsa yake fadin *( D'an Adam tara yake bai cika goma ba)* Allah yai mata komai amma bata da kyawun hali.

Babu yabo babu fallasa yai mata sallama........Gabanta ya fadi ganin yana jan kafarsa babu ma takalmi sai safa kawai! kafafun, yana tafiya da d'ya yana dingisa daya, ta tsirawa kafafun ido har ya k'araso kusa da ita bata sani ba.

Babu walwala a tare dashi yace." Zan fita gurin aiki ina fatan baki matsala."?

Idonta ta janye tana jin wani irin a tare da ita.......Ashe rauni yaji mai yawa! cikin zuciyarta take maganar..

Ganin ba tace komai ba kawai sai ya kama hanyar fita.

Ta bishi da kallo 'kwalla na ciko idonta.....duk abunda tai masa shi ya janyo.......Idan ta tuna abunda ya faru kamar ta mutu da bakin ciki.

Bai shiga headquarter nasu ba, sai da yaje asibitin ya dubata, babu shakka yaji dadin yanda ya ganta tayi garau! suna hira da Uwale. wacce take kwantar mata da hankali gami da bata tabbacin cewa ta kwantar da hankalinta Umaru kamar ya aureta ya gama.

Maganganun Uwale sune suka sanyayar mata da zuciya.....Shi kansa likitan dake dubata yaji dadi sosai. nan ya cigaba da bata shawarwari masu kyau.........

*Kuyi hakuri ina zuwa makaranta, shine dalilin da yasa bakwa samun update akan lokaci NAGODE🙏🏻*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  4k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*91&92*
Wannan ciwon jikin da ya fita dashi   ashe sa hannun zazzabi ne. domin koda ya zauna a ofis din kasa katabus! yayi kawai sai  ya koma kan doguwar kujera ya kwanta zazzabin na sake k'arfi a jikinsa wani irin bacci mara dadi yana fizgarsa.
Shigowar Asp ofis din ne ya zaburar dashi! ya bude jajayen idanuwansa yana kallonsa har ya k'araso gurinsa da wasu takardu a hannunsa.

Ganinshi wani iri ya sanyayar masa da jiki da ya shigo da 'kwarin gwiwa sakamakon samun rahoton mutumin da suke ta nema ruwa a jallo.

Gefansa ya zauna da fadin." Jarumi wai shin me yake damunka ne tuntuni nake kiran wayarka babu amsa wannan dalilin ya sanya kawai na yanke shawarar zuwa ofis din naka.

Ya mike zaune da 'kyar! yana ya mutse fuskarsa yace." Bana jin dadin jikina wallahi zazzabi da ciwon jiki ke damuna."

Maganar yake amma shi Asp din hankalinsa yana kan k'afarsa dake kumbure!

Cike da al-ajabi  yace." Rauni kaji ne babu labari."?

Mirmushi takaici yayi yana danne b'acin ran dake taso masa yace." Jiya bayan rabuwarmu ina shiga gidan.......duk ya kwashe komai ya fada masa.

Ya dinga girgiza kansa yana mamakin al'amarin yace." Yanzu Zinatu da hankalinta ta aikata wannan d'anyan hukunci. koda yake ko shakka ba nayi da sanya hannun Zainab domin yini sukayi a tare wa yasan irin abunda suka shirya.

Ya girgixa kansa da fadin." Kada ka zargi kowa domin yarinyar abunda yafi haka ma zata aikata, na shiga dakina na samu ta tarwatsa min ko'ina wannan shine dalilin da ya sanya na samu rauni a kafata.

Yace." To wai shin ma me ya had'a ku ne har hakan ta faru."?

Tsaki yaja kafin yace." Bak'in kishi ne da jahilcin dake damunta, tana zargi na dan haka zuciyarta take raya mata, amma ni nasan abunda na aikata ba haram bane domin da niyyar taimako nayi kuma ko'ina hakan na iya faruwa ballanatana a cikin gidana, Asp mutukar naga abunda zai cutar da wani musulmi dan uwana mace ko namiji sai inda karfi na ya kare."

Yace." Maganar kake a du'kun'kune ka fayyace min makasudin abunda ya janyo matsalar."

Kallonsa yayi na second biyu kafin ya fara warware masa abunda ya faru.

Yace." Gaskiya ne baka aikata haramci ba kamar yanda take zarginka, kayi hakan ne da niyyar taimako amma kasan mata idonsa yakan rufe akan kishi basa tunani akan kowa sai a kansu amma meye laifinka dan ka dauki Hamra'u kasa a mota shin so take ka bari ta mutu ko yaya."?

Yace." Nima dai haka na gani meye laifina anan? wallahi banyi hakan da wata manufa ba sai da niyyar taimakon musulunci."

Yace." Umaru wallahi kwata-kwata bana k'aunar alakar Zainab da Zinatu domin dukkaninsu basu da kirki! maganar dai guda daya ce akwai sanya hannun Zeey dangane da faruwar hakan kuma zanje gidan na sameta."

Yace." Aa kada ka yanke hukunci cikin fushi! na fada maka fa cewa.......Koda babu Zainab a cikin rayuwar *ZINA* to zata iya aikata abunda yafi haka wannan shine dalilin da yasa tun kafin muyi aure nake da shakku akanta saboda gudun faruwar matsala irin wannan......Ban auri Hamra'u ba haka tana faruwa to inaga kuma na aure ta."?

Yace." Kai  dai zaka zage damtse ka  tsaya a matsayinka na namiji ka nuna mata bambanci sosai amma naga duk ka wani susuce! wai shin ko tsoronta kakeji ne."?

Murmushin takaici yayi kafin yace." Asp mu rufe maganar nan dan Allah! muyi abunda zai yuwu domin  ina so na tafi gida na kwanta na huta."

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Ai shikkenan tunda ka fadi haka amma ni kam dole na tauna tsakuwa domin aya taji tsoro."

Shuru kawai yayi masa yana jin wani irin takaici a ransa.........Wai yana tsoron yarinyar, wannan maganar ta sosa masa rai mutu'ka! shin akwai wata mace da zai ji tsoro a fadin duniya, Uwarsa ce kuma bata raye.

Takardun dake hannunsa yake bud'ewa, wata doguwar takarda ya fito da ita da hoto kati daya, mika masa yayi kafin yace." Ka duba hoton sosai ka kuma duba rahoton dake jikin takardar.

Saman takardar kawai ya duba yaga an sanya *AMINIYA GIDAN JARIDA KANO STATE*

Ya kalleshi da fadin." Wani abu ne yake faruwa a jahar *KANO."?*

Yace." Duba dai amma ka fara nazarin hoton mutumin dake hannunka."

Ya 'kurawa hoton ido yana ta so ya hasaso kowaye.....ya girgiza kansa da fadin." Bangane waye ba wallahi."

Asp din ya kar'bi hoton da fadin........
*UBAN DABA NE."!* A zabure!  ya kar'bi hoton yana sake dubawa, kafin kice kwabo gumi ya fara tsatstsafowa a saman goshinsa.

Tabbas idan ba wanda yayi masa farin sani ba ba zai ganeshi ba domin duk kammaninsa sun sauya......duk babu wannan 'kasumbar!  yana sanye da kayan hausawa riga da wando harda hula sai dai jikinsa lullube yake da wani farin mayafi irin na maza wannan shi ya hana bayyanar nakasar dake tare dashi .........Tabbas shine domin k'wayar idonsa basu sanja ba suna nan yanda suke gwala-gwala masu tsananin ja! kamar garwashin wuta!

Ya kalli Asp din da fadin." Ya akayi yanzu meye abin yi."?

Asp din yace." Nafiso ka karanta rahotannin kafin mu tsaya a matsaya ana bincike ne a kansa da yaransa da suka sauka a garin.

Ya mayar da hankalinsa kan takardar yana karantawa.

Rahoto ne daga gidan jaridar *AMINIYA* cewa wasu 'yan gudun hijira da suka samu masauki a k'auye *KUYAN TA INNAH* ana zarginsu da ta'addanci tare da yiwa k'ananun yara fyad'e........Ana dai binkice a kansu domin tabbatar da gaskiya magana.

Ya share zufar saman goshinsa, ya kalli Asp din da fadin." Ko shakka ba nayi zasu aikata abunda yafi haka, babu wani maganar binkice! wai shin me yasa jami'an tsaron *KANO!* suke da sakaci ne? to ni da kaina zan shiga Kanon domin a gudanar da binkicen dani idan ba haka ba zasu iya kyaleshi ya cigaba da ta'addanci tare da kashe rayukan da basu ji basu gani ba." Murmushi Asp din yayi kafin yace." Kai ka fiye gaggawa! yanzu idan akayi wani yun'kuri zasu ankara su samu damar tserewa.....wannan rahoton babu wanda ya san dashi sai ni da kai sai kuma Commissioner.......Domin Abokina *Wali Nasiru* dake *KANO* tare da sauran abokan aikinsa ne suka shiga 'kauyen suna binkice akan matsaltsalun dake faruwa.....nan suka samu cikakkaken bayani daga bakin wani dattijo cewa tsayin shekara dari da wani abu wata gagarimar matsala bata ta'ba faruwa ba a 'kauyen sai dalilin zuwan 'yan gudun hijirar.......Dalilin da yasa kenan suka tsananta binkice akansu domin gano gaskiyar lamari.......Kasan abokina ne sosai tare mu kayi karatu to yana bani labarin abunda ke faruwa sai na bukaci da ya turo min rahoton domin ni kaina sai da na zargin wani abu, saboda haka muyi hakuri kada muyi gaggawa domin hakan zai zaburar dasu, su gudu! a nutse zamu kamasu. ina kuma kara tabbatar maka da cewar babu wanda ya san wannan rahoton daga ni sai kai sai kuma mai gayya mai aiki don bana tsammanin ma gwamnati tasan da abunda ke faruwa domin yanzu muka gama tattaunawa commissioner din akan hakan."

Dogon tsaki! yaja ransa duk a dagule! wane irin aikin gaggawa ai a ganinsa jinkiri shi zai cutar dasu, ya ga dama sun samu amma za suyi wasa da ita! ya dinga jan tsaki! kansa ya cigaba da sarawa! tabbas da ba dan a karkashin gwamnati yake aiki ba to da babu shakka yau zai yiwa garin *KANO* dirar mikiya duk inda *UBAN DABA!* Da yaransa suke sai ya lalubo su domin gwabzawa!

Asp din yace." Ya kamata kaje gida ka huta idan zai yuwu ma gobe ka zauna ka sake jin 'kwarin jikin ka Allah ya sawwake."

Ya amsa da "Ameen yana duba agogon dake daure a hannunsa, uku da rabi na yamma....Asp din ya mike da niyyar fita shima mikewar yayi, ya dauki gilas dinsa ya sakaye idonshi kafin yabi bayan Asp din da niyyar zuwa gida ya sha magani ya kwanta ya huta.

'Bangaranta kuwa tunda ya fita ta kasa samun nutsuwa, tana ji kamar ta kira shi a waya tana kuma tunanin kada ta zubar da ajinta.....Haka ta dinga juye-juye a saman gado sa'i da lokaci

tana share hawayen takaici!  ita kanta ba'a son ranta ta aikata masa hakan ba, kawai ya b'ata mata rai ne.

Kafin ya shiga gidan sai da ya gabatar da sallar la'asar tukkuna.........Ya duba gurin su Uwale domin ya tabbatar da cewa sun fito daga asibitin saboda a d'azu da safen Likitan yake tabbatar masa da cewa zai sallamesu zai kuma sanya direba ya kai su gida.

Sosai yayi farin cikin ganinsu A falo suna hira har ita Hamra'u domin ta wartsake kamar ba ita ba, hakan duk ya faru ne dalilin kwantar mata da hankali da Uwale keyi ta tabbatar mata da cewa suna zuwa k'auye  manya zasu tsayar da maganar daurin auransu, wannan ne dalilin da yasa ta samu nutsuwa ta kuma kwantar da hankalinta.

Gabadaya suka dinga bin sa da kallo har ya samu guri ya zauna.......Uwale ce ta magantu, cikin damuwa tace." UMARU mai ya samu 'kafar ka."?

Shuru yayi na minti biyu kafin yace." Na d'an taka k'usa ne  kin san tana da dafi! shine dalilin da yasa kafar ta kumbura!

Sosai tayi mamaki kafin tace." Cikin wannan uban takalmin da kake sanyawa har kusa ta iya huda maka 'kafa UMARU anya kuwa."?

Murmushi yayi da fadin." Uwale ki bar tsautsayi kawai! Allah ne kawai ya takaita min wahala 'kusar bata shiga sosai ba ku cigaba da yi min addua."

Tace."To Allah ya kiyaye ya tsare gabanka da bayanka."

Ya amsa da "Ameen ya rabbi  kafin ya kalli Hamra'u da tunda suka fara maganar ba tace komai ba.

Ya dan saki fuskarsa da fadin." Ya jikin naki."?

Tace." Da sauki Yaya na, kai ma ya jikin naka? Allah kiyaye gaba."

Ya amsa da "Ameen ya rabbi nagode sosai amma kin dai ji abunda likita yace miki ko? ki rage tunani dasa damuwa a ranki."

Tace." To Yaya na insha Allah zan kiyaye nagode Allah ya saka da alkairi."

Bece komai ba ya kalli Uwale da fadin." Uwale a dan bani  abinci zanci kafin nasha magani."

Ko kafin Uwalen ma tace komai zumbur ta mike ta  kama hanyar kicin......Gabadaya suka bita da kallo suna girgiza kai, tausayi take basu.

Yaci abincin sosai yayi godiya ga Allah kafin ya wuce sashensa dan beyi niyyar shiga gurinta ba gudun b'acin rai!  abunda baya bukata kenan.

Marakisiyya dake shanya kayan data wanke a harabar gurin ita taga wuce war sa, ta dur'kusa har kasa tana gaisheshi ya amsa ba tare da ya kalleta ba,  ya wuce ya bar ta a gurin.

Ita din ke shedawa uwar dakin nata dawowar mijin nata.........Tace mata ta ganshi ya fito daga sashen masu gidan ko za'a kai masa abinci."

Ranta ya 'baci!  ta kalli Marakisiyyar ta watsar kafin ta buga mata tsawa! had'e da nuna mata hanyar fita.

Da sauri ta mike ta kama hanyar fita gabanta na faduwa! sam ba tayi tsammanin cewar maganarta zata fusata! Uwar dakin nata ba, a ganinta kamar gwaninta tayi.

Ita kuwa har Marakisiyyar ta fita ba daina hararar hanyar data bi ba.......Wani irin kishi ne yake damunta. wannan ai abun kunya ne mijinta ya dawo amma ace mai'aikinta ce ke sheda mata, bayan haka kuma tana jin haushin abunda ya kai shi sashen masu gidan, hakan baya rasa nasaba da mutsiyaciyar yarinyar data tsana a rayuwarta.

Sabon wanka tayi....... sosai tai gayu tayi cikin kananun 'kaya masu daukar hankali, masifaffun turarukan da take  d'aukar hankalinsa dasu tasa a kowane sassah na jikinta,  kai tsaye sashen ta nufa zuciyarta cike da wasiwahsi!

Idar da sallarsa kenan domin tun daga magaribar har isha'in a gida ya gabatar bai samu shiga massalaci ba dalilin matsanta masa da kafarsa tayi, koda yake yasha  magani da sauki akan da.

Kamar bata so tayi masa sallama,  shima  babu yabo babu fallasa ya amsa, yana bin ta da kallo har ta samu saman kujera ta zauna.

Shuru tayi tana dan wasa da yatsun hannunta!.....shi kuma bai fasa kallonta ba, da carbi a hannunsa yana ja yana nazarinta.

Ta d'ago kai suka had'a ido!  bai janye idonsa ba bai kuma ce mata komai ba......Itace dai ta janye idonta sakamakon dafin idanuwansa dake kokarin kassara ta!

Da 'kyar ta iya bude baki tace." Ashe ka dawo."?

Uffan bece mata ba kawai dai ya zuba mata idonsa dasu yake hukuntata!

Ta kalleshi a karo na biyu idonsu ya sake had'uwa.......Wani abu mai yuwar fassaruwa take hange a cikin kwayoyin idanuwansa, gabadaya jikinta ya mutu sai kawai hawaye ya kwace mata! suna zuba tana sa hannu tana sharewa tare da shak'ar hanci! tabbas da tana da iko da sai ta dawo da ciwon jikinta a ganinta ma kamar ta fishi damuwa!

Gyaran murya yayi kafin yace." Me kuma nayi miki? zaki sanya ni a gaba kina kuka! ai ni zanyi kuka duba da ta'addancin da ki kayi min."

Ta kalleshi hawaye share-share! "Nice 'yar ta'addah."? tafada tana nuna kirjinta.

Kansa ya daga da fadin." Eh mana baki da imani! idan ba haka ba mai zai sanya ki farfasa min kwalabe a daki ai kinso ki cutar dani ne."

Taja hanci tana goge ragowar hawayen daya rage  tace." Okey kai yanzu a ganinka abunda ka aikata shine dai-dai."?

Ya ajiye carbin dake hannunsa sosai ya mayar da hankalinsa kanta yace." Me nayi ? ina so kiyi min cikakken bayanin abinda nai miki  ko'ina akaje baki da hujja!

"Shikkenan tunda haka kace ni bazan yi wata magana da kai ba a yanzu amma ina mai tabbatar maka da cewa wallahi idan baka daina ba nima ba zan fasa ba."!

Yace." Idan kuma  ta hanyar halak nayi fa? shin ko zaki hana ni aikata sunnah da matata."?

Shuru tayi tana kallonsa gabanta in banda faduwa babu abunda yake.

Yace." Ki kiyaye domin kishin hauka babu inda zai kai ki,  sai halaka hakan kuma da kike bashi zai ha nani abunda nayi niyya ba."

Jikinta duk ya mutu da maganarsa, a sanyaye tace." Kayi hakuri."

Wani sanyi ya ziyarci zuciyarsa.......Lallai ya yarda da maganar Uwale da Asp in da  suke cewa cikin laluma ake nusar da mutum idan yana aikata kuskure......gashi kuwa yayi amfani da damar bukatarsa ta biya bai ta'ba tsammanin zata bashi hakuri ba, koda yake yabi hanyar da hakan zata kasance!

Yace."Na yafe miki Allah yayi miki albarka."

Ta amsa da "Ameen Nagode."

D'akin yayi shuru na 'yan mintina kafin tace." Kaci abinci."?

Yace." Eh naci gurinsu Uwale yanzu kwanciya kawai nake bukata."

A hankali ta mike ta iske inda yake zaune.........Hijab din jikinta ta cire kafin ta zauna kusa dashi..........Kallonta kawai yake yana sha'kar kamshin jikinta da yake masifar so!! idonta kuri kan k'afarsa kafin ta kai hannu gurin ciwon!

Da sauri ya janye yana ya mutse fuskarsa!

Tace."Da zafi ko."?

K'amar karamin yaro ya daga kansa!

Sai kawai ta taya 'bera 'bari ta janyoshi jikinta kansa ta rungume a kirjinsa tana jijjigashi tare da shafa sumar kanshi kamar k'aramin yaro!

Tabbb! ☺ ai neman ciwo yayi ya rasa irin wannan soyayya! haka   mai neman kuka an jefeshi da kashin awaki!  mutumin da ake rarrashi!  domin yayi bacci sai kawai ya 'buge da kusurkusur yana motsi tamkar yaron dake tsananin  bukatar nono! haka ya dinga cusa fuskarsa a kirjinta da wayo da dubara ya 'balle bireziyar ya sa'bule! 'karamar rigar dake jikinta........Daga nan labari ya sauya.🤭

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: *Assalamu alaikum warahmatullahi masoya yan uwa na musulmai...*
🐫🐫🐫🐫🐫
🐫🐫🐫🐫
🐫🐫🐫
🐫🐫
🐫
*Tabbas wani kaya sai amali ,busa sai sarewa jiniya sai a gidan gomna ,ina kuke mata ma'abota tambayar ina wannan shahararriyar y'ar mutan nijer wato mali ,wacce akafi ma lak'abi da...*```🐫BUZHUWA EMPIRE🐫```
*Ina kuke matan Aure n mu masu fuskantar tangard'a tare da k'alubale a gidan mazajen Auren mu??💃💃.*
*Ina kuma y'ammata masu buk'atar farin jini ta hanyar samun mijin Aure?? Don raya sunnar manzon mu SAW...Nasan duk kunce gamuuu!!!👆👆👆.*  *Gafa BUZHUWA EMPIRE ta* *taho maku duk don share hawayen dake kwaranya akan fuskokin ku ta hanyar kawo maku sirrin mallaka tare da* *magani ,haka ma y'ammata ga sirrika nan da maganin shi ,wanda anyi mutane babu adadi kuma anzo anyi* *godiya....ki tambaya wacece Buzhuwa empire ga dukkan wanda* *yasanta ,zakuji karin bayani daganan. Muna bada mallaka ta hanyayoyi dabam* *dabam ,wanda da alfarman annabin rahma xamu sha mmki.* *Mallakar tamu akwai na 3k akwai na 5k ,akwai na 10k da sama ma da haka. Mudai fatan mu shine babu cuta babu cutarwa , kamun mu biya* *maki bukatanki sai kin mana rantsuwa akan bazaki cutar dakowa* *ba ,mallaka matan aure muke ba zallah. Na farin jini kuma na y'ammata ne ,shi munayin shi akan 5k ne da kuma na 10k.* *Zakuna iya tuntu6an wannan numbern domun karin bayani...09061466409/08081202932.*
*Ga kad'an daga cikin mallakar da muke amfani wajen yinsu👇.*
*Mallaka ta hanyar K'wai.*
*Mallaka ta hanyar nono*
*Mallaka ta hanyar zobe*
*Mallaka ta hanyar guru*
*Mallaka ta hanyar turaruka da dai sauran su.... Sai kin taho domun share hawayenki daga kunci zuwa farin ciki....* ```BUZHUWA EMPIRE taku ce!!!```
~08081202932 ko 09061466409~

*93&94*
A daran rigima ce ta kaure tsakanin Asp da Zeey sosai yayi mata jan ido ya kuma tabbatar mata da cewar kwa'bar ta tayi ruwa,  amma ta kwana da shirin cewa mutukar da sanya hannunta auran yar mutane ya mutu to itama ta kwana da shirin nata auran sunansa matacce.

Al'amarin ya bata mamaki sosai, domin ba tayi tsammanin matakin da zata dauka ba kenan, tasan dai sunyi zantuka da yarinyar,  ta kuma bata shawarwari! amma kuma koda wasa ba tayi tunanin cewa za ta cutar da mijin nata ba.

Jikinta duk ya mutu dan tunda take da mijinta bai ta'ba ci mata mutunci irin yau ba, lallai babu shakka dole tayi takatsantsan gudun faruwar wata matsalar  domin ta fahimci mijin nata a fusace yake,  hakuri ta bashi da fadin." hakan ba zata sake faruwa ba, ko sauraranta beyi ba ya kama hanya yayi tafiyarsa gidan Madam tunda dama a can yake.

Karfe uku da rabi na dare.....Gidan jaridar *AMINIYA*  ya tashi da wuta!  wacce ba'a san abunda ya haddasa ta ba,  tashin hankali kenan! wutar sai da taci mutum hudu masu aikin kwana 'kurmus!  suka mutu dan da 'kyar aka samu gawarsu........Wannan ibtila'in da ya faru ya tashi hankali jama'ar gari gabadaya gari ya dauka da maganar...... mahukunta kuwa sun tsananta binkice domin gano abunda ya haddasa tashin wutar.

Wayewar gari a cikin k'auyen sukayi 'batan dabo! shi da jama'arsa sama ko kasa aka neme su aka rasa.....sun gudu bayan sun tafka ta'addanci dan gabadaya sai da suka yashe jama'ar garin, da yake k'auye ne basu  waye  da kai kudi banki ba, a gida suke ajiyewa, wannan dalilin yasa suka bi dare suka haura gidajen mutane suka tafka musu sata,  kudi cikin jakar baggo suka fita daga cikin garin.

Wannan ne ya tabbatar da zargin da ake musu.....Mane ma labarai suka fara d'aukar rahotanni daga bakunan jama'ar kauyen  suna watsawa a duniya.....Jami'an tsaro kam basu zauna ba sun bazama domin binkicen inda suke.

Wannan labarin yayi masifar 'batawa UMARU rai dan koda Asp din yake sheda masa abunda yake faruwa, tsaki kawai yaja ya kashe wayarsa, shi kansa Asp din haushinsa yake ji domin da yabi shawararsa a ganinsa da duk haka bata faru ba.

Ta fito daga toilet ta sameshi ya dafe kai sai sakin tsaki yake.....Cike da damuwa ta dafa kafadarsa nan taji yanda jikinsa yake  mazari da tsuma!

A sanyaye tace." 'Kafar ce take damunka."?

Kallonta yayi...sai ta kasa hada ido dashi ganin yanda gabadaya kwayoyin idonsa suka sauya jijiyoyin kansa sunyi rad'a-rad'a! lallai da akwai abunda yake faruwa!

Tana kokarin magana ya mike tsaye.... ya kai ya kawo a dakin! fatar goshinsa duk ta tattare ta tara zufa!

Hankalinta ya tashi domin duk sanda ya shiga irin wannan yanayin abunda zai faru ba zai kyau ba.

Cikin dauriya ta 'karasa inda yake kokari take ta rungumeshi amma hakan ya gagara! domin gabadaya ya kasa tsayuwa a guri guda.

Sai kawai ta fashe da kuka da fadin." Wai meye haka ? ni bana san ganinka a irin wannan yanayin idan nai maka laifi kayi hakuri."

Bece mata komai ba gefe ya matsa yana kokarin cire rigar jikinsa......Ta tsira masa ido dake cike fargaba da tashin hankali!

Gabadaya jikinsa ya bude mussaman kirjinsa da damtsan hannuwansa sai rawa jikin yake ruwan gumi na diga.

Da sauri taje ta dauki wayarta, Asp zata kira ta sheda masa abunda yake shirin faruwa domin ta tsorata da ganin ya cire riga.

Kafin ma ta kai ga kiran Asp din ya kwarma ihun!!! da ya sanya wayar hannunta fad'uwa, ta juya da sauri! kawai sai ta ga har ya cire zabgegiyar wukar dake rataye a dakin.......Ya fara da dadurawa! a jikinsa, mussaman wuyansa.......

Ita kam tana ganin tashin hankali a rayuwarta! a kid'ime ta nemo number Asp din sai dai a kashe take...........Ta juya ta sake kallonsa, bai fasa dadurawa jikinsa wuka ba yanayi yana taune bakinsa.

Auran d'an tauri akwai tashin hankali! wallahi ita ta d'auka tuntuni ya bar harkar ganin ya kwana biyu beyi ba.

Tsabar fargaba k'afafunta kasa daukar ta sukayi kawai ta zube kasan kafet ta takure jikinta guri

daya ta fashe da wani irin kuka! babban tashin hankalinta taga yana gurzawa jikinsa wuka gani take idan rana ta 'baci wukar zata samu nasara!

Can ta hango wayarsa saman kujera, da sauri taje ta dauka, number Asp din dai ta nemo ta kira shi, aka ci sa'a wayar ta shiga, tana kuka take sheda masa abunda yake faruwa......da yake weakened ne yana gida ko minti goma ba'ayi ba ya shigo gidan.......ita ta shiga dashi Dakin tana nuna masa shi yana nan yana Aikin abu daya ko gezau! domin wani irin karfi da kwarin jiki yake ji a duk lokacin da wukar ta sauka a jikinsa.

Asp din ya durfafeshi da fadin." Ya isa haka! ni da nasan abinda zai faru kenan, da ban fada maka ba, nasan dole ranka ya 'baci amma ai basu tsira ba da ikon Allah sai bukatarmu ta biya a kansu.

Kasa hakuri tayi ta karasa gurin tana tambayar Asp din abunda yake faruwa.........kasa bata amsa yayi domin a lokacin burinsa kawai yaga ya samu kan abokin nasa.

Da 'kyar ya iya zaunar dashi gefan gado ya mayar da wukar gidanta rataye ta yayi a gurinta, ya dawo ya zauna a kusa dashi.

Sai suka sanyashi a tsakiya, dukkaninsu babu wanda baya jin sautin fitar numfashinsa huci kawai yake yana hura hanci!

Ita kam jikinsa kawai take kallo domin ganin koda akwai rauni babu wata matsala fatar jikinsa tana nan a inda take.

Asp hannu yasa cikin aljihunsa kwalin Sigari ya fito dashi da leta ya kunna masa, aikuwa zuka uku yayi mata ta kare, ya sake kunna masa wata, a kalla sai da yasha kara biyar sannan ya dawo hayyacinsa...............Asp ya kalleta da fadin." Ta had'a masa ruwan wanka.

Da sauri ta kama hanyar band'akin duk jikinta a sanyaye!

Ya kalleshi da rinannun idanuwansa a kausashe yace." Jiya nayi magana kace ina da gaggawa! yanzu me jinkirin ya haifar."?

Ya dafa kafad'arsa da fadin." Kai dai da kawai akwai lauje cikin nad'i! domin Wali Nasiru ya sheda min duk abunda ke faruwa akwai sanya Hannun manyanmu dangane da faruwar al'amarin.

Yace." Kai wa kake zargi."?

Shuru yayi na minti biyu kafin yace." Commissioner domin har yanzu bai kira ni yace min komai ba, kuma ina da tabbacin cewa yasan abunda yake faruwa.

Yace." Shikkenan yanzu mutanan sun dinga samun nasara da sa'a kenan! me yasa ba zamu sadaukar da rayuwarmu akan ganin mun kawo karshen su ba......Akan wannan dalilin fa wallahi zan iya ajiye wannan aikin."

Yace." Haba kada kayi haka abokina kabi komai a sannu a hankali, insha Allah komai zai daidaita za kuma mu samu nasarar kama wa'innan mutane, saboda haka mu cigaba da addua da kuma bincike akansu."

Shuru kawai yayi masa domin har yanzu akwai sauran takaici a tare dashi...............Ta fito daga toilet din tana sheda masa cewa ta hada ruwan.

Ba tare da yace komai ba ya tashi ya kama hanyar toilet din, sai ta  rufa masa baya, ganin haka yasa Asp din tafiya gida gabadaya shima ranshi a bace yake da faruwar al'amarin.

Taimaka masa tayi yayi wankan suka fito a tare.

A sanyaye take goge masa jiki da towel sai kallonsa take tana wasu tunane tunane a ranta mutum sai kace mai aljanu ita yanzu tsoro ma yake bata.

Kallon da take masa ne ya dameshi ya juyo suka hada ido.

Sunkuyar da kanta tayi ta shafo mai a hannunta ta fara shafa masa a gadon bayansa.

A hankali tace." Wai me ya faru ne hankalina yana tashi a duk sanda ka shiga irin  wannan yanayin bana so ko kadan."

Hannunta ya riko  yana kallonta idonta ya tara kwalla, da gaske bata so domin ya ga hakan a cikin kwayar idonta.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke kafin ya shiga warware mata abunda yake faruwa.

A tsorace take kallonsa kafin tace." Kayi wa Allah da Annabi kada kasa kanka a cikin wannan al'amari domin muna sonka kada ka mayar damu marayu." Murya na rawa take maganar.

Ya dunga kallonta yana jin wani irin sonta na ratsa jikinsa!

Fad'uwar gaba asarar namiji! dashi da *UBAN DABA!* Yanzu aka fara! har sai yaga abunda ya turewa buzu nadi........a zuciyarsa yake wannan maganar, a zahiri kuwa ganin yanda duk hankalinta ya tashi yasa ya sassauta muryarsa yana rarrashinta, sai ya kasance suna rarrashin juna ita dai burinta yay mata alkawari cewa ya bar harkar *TAURI!* Kuma bai zai tunkari *UBAN DABA!* ba.

Alkawarin gaibu yayi mata domin ta samu nutsuwa! amma baya tsammanin zai janye kudirinsa! harkar *Tauri* kuwa wannan a jinin jikinsa take.

Yayi mata alkawarin ya bari, amma abun mamaki taji yana waya da babban yaronsa *ALBA* yace lallai - lallai gobe ya kawo masa maciji yana bukatarsa.

Cikin faduwar gaba take kallonsa har ya 'kare wayar ya ajiye a gefansa.......Ta 'bata rai da fadin." A'a ina za'a kawo maciji kuma me za kayi dashi."?

Yace." Ina bukatarsa ne babu ruwanki dashi."

A raunane! tace." Yanzu fa kayi alkawari ka daina wannan harkar, me yasa duk ga dabbobi ne wanda Allah ya hallata ba zaka ci ba sai maciji me kukeji a jikinsa."?

Ya d'aga mata hannu da fadin." Kinga *ZINA* kada ki dameni dan Allah ba fa zaki ha nani aikata abunda na taso dashi tsayin shekaru da yawa ba, saboda haka ki cire kanki daga wannan sabgar."

Rai a b'ace! ta kama hanya ta fice daga d'akin, tana Allah wadai da al'amarin.

Tsayin sati suna 'yar tsama a tsakaninsu domin tun ranar da ta fita daga dakinsa bata sake shiga ba, kowa a dakinsa yake rayuwa, shima bai nemata ba sai da ya tabbatar da cewar ya cinye miyar macijinsa sannan ya nemi in da take da bukatarsa domin dauriya kawai yake a tsayin kwanakin.

Tace bata san wannan ba, domin data kalleshi zata dinga hasaso shi yana cin maciji sai zuciyarta ta tashi, takai ta kawo ma duk sanda yayi yunkurin sumbatar bakinta sai ta kwara amai na bam mamaki!

Al'amarin ya dinga dugunzuma masa zuciya yana bala'in jin haushi yaje da bukatarsa ta dinga gudunsa gashi sam baya son ya dinga gwada mata k'arfi! yafiso suyi komai cikin walwala da farin ciki.

Yau dai shiri na mussaman yayi kafin ya tunkari inda take sai da yayi wanka da turaruka bakinsa sai kamshi yake fitarwa shigar da yayi ma ta mussaman ce, domin wasu kayan bacci yasa masu kyau da daukar hankali.

Tana kwance kan gado abun duniya ya isheta kwana biyu ta kasa gane kanta, komai na duniya yayi mata zafi ta rasa yanda za tayi da rayuwarta.............Yawan tashin zuciyar da take yana damunta.

Shigowarsa dakin yasa da sauri ta juyar da kanta, sam bata san Kallon fuskarsa.

Cikin bargon da take ciki ya shiga yana lumshe mata ido, kokarin janyota yake tayi sauri tashi tana yamutse fuskarta........Yawu ne ya taru a bakinta ta sauka daga gadon toilet ta nufa ta zubar da yawun ta dawo.

Abun ya bashi haushi mutuka! ya rufeta da fada ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba.

Hannu ta daga masa da fadin." Don Allah ka kyaleni haka, ni wallahi gabadaya yanzu bana san damuwa, kai kuma na lura duk sanda ka shigo dakin nan sai ka 'bata min rai! kawai ka daina shigo min daki."

Ya mike zaune yana mata wani irin kallo kafin yace." Iskancin banza da wofi! meye abun k'yama a jikina da har kike tara yawu!  na dauka yau kwana takwas rabon da ki bani hakkina na aure ina ruwanki da tsarin rayuwata maciji ni naci abina mai zai dameki kuma."

Tace." Ni fa ba maganar maciji nake maka ba, kai din ne kawai bana son gani." da gaskiyarta take maganar.

Takaici da bacin rai sukayi masa katutu!  ya daina jin tausayinta kuma duk abunda za tayi sai ya biya bukatarsa.

A daran bai saurara mata ba ya turmusheta ya zage dukkakin karfinsa a kanta, ya galabaitar da ita sosai domin dama yakan dade kafin ya kawo haka hallitarsa take da nisa.

Aikuwa da ciwo ta tashi dan rasa gane kanta yayi.....babu shiri ya kira likiti domin ya duba masa ita.

Kallon farko likitan ya gane abunda ke da akwai amma bai tabbatar ba sai da ya auna fitsarinta.....nan ya tabbatar da zarginsa, ciki ne sati bakwai da kwanaki.

Sai ya rasa ina zai sanya ransa yaji dadi, kawai ya shiga godewa likitan kamar shi yayi masa kyautar cikin, kudi ya fito dasu daga aljihu ya bawa likitan yana godiya.

A ranar sai bayan azuhur yaje gurin aiki, yana tare da ita yana rarrashinta da kalamai na so da k'auna,  ita dai jinsa kawai take tana mamakin al'amarin, dama jikinta sai da ya b'ata cewa hakan na iya faruwa aikuwa gashi hakan ta kasance.....ita kam bata shirya haihuwa yanzu ba, tunda beyi k'wari ba tasan yanda za tayi ta zubar dashi.

Koda ya dawo daga gurin aiki sashenta ya nufa domin dubata,  ya same ta fes da ita domin duk jin jikin da take bata fasa ado da kwalliya ba hakan kamar ya zame mata jiki.

Ya zauna kusa da ita yana nanikar jikinta, shi yana bala'in san kamshin ta ita kuma tana gudunsa, ba komai ne ya janyo hakan ba, sai d'an tayin  cikin dake kwance a kasan mararta.

Be damu da yanda take kauce-kauce ba, ya dinga sumbatar fuskarta yana ta so ya hada bakinsa da nata tana kaucewa.......da kyar ya samu nasara! tunda ya kama harshen be saki ba sai da ya gamsu tukkuna.

Idonta ya ciko da ruwan hawaye harara kawai take zabga masa ta rasa wane irin mara zuciya ne shi.

Ido jawur! yace." Ya jikin ina fatan kin wuni lafiya tare da babyna."

Shuru tai masa tana dauke kanta.

Ya sauke zazzafar ajiyar zuciya tare da kallon agogon dake daure a hannunsa, magariba ta gabato, tsaye ya mike ya dan kalleta tana ta yamutse - yamutse! huci ya fesar! kafin ya kama hanyar fita, tabi shi da kallo tana zum'bura bakinta.

Kasa daurewa yayi ya bar maganar a ransa a daran ya shedawa Uwale, farin ciki kamar ya kasheta, tace." Lallai kace da kwarin gwiwarmu za mu shiga k'auyen *K'afur!* ai wannan abun alkairi ne da ya kamata ace yan uwa sun sani.

Murmushi kawai yayi da fadin." Saura kwana nawa bikin ne."?

Tace." Ashe baka lissafi ai yau saura kwana uku mu tafi dan duk wasu shirye-shirye mun kammala."

Yace." To Allah ya kaimu amma ni ina tsammanin a ranar zan dawo bayan an daura aure."

Tace." To babu damuwa amma ita matar taka sai ka bar ta tare damu domin 'yan uwa su kara sanin ta."

Yace." Shikkenan haka za'ayi insha Allah."

Sallama sukayi da juna kai tsaye da ya fito sashen Gimbiyar ya nufa cike da farin cikin kasantuwa da ita.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin

karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*97&98*
Wani irin bacci sukayi mara dad'i sakamakon damuwar da suke ciki. da yake namiji ne shi yakan iya danne damuwarsa ita kam ta kasa dannewa domin  gabadaya jin kanta take a takure! ita akan kin kanta tasan yun'kurin da tayi ba mai kyau ba ne, shiyasa take bala'in jin kunyar hada id'o dashi!

Kwance ya sameta saman gado tun bayan sallar asubahi ta kwanta tana k'okarin gayyatar bacci yaki zuwa babu shi ma gabad'aya a idonta tunani yafi yawa a tare da ita.

Ido ta tsira masa har ya k'araso bakin gadon, ya shirya tsaf da niyyar fita gurin aiki.

Babu yabo babu fallasa ya kalleta da fadin."  kin tashi lafiya."?

A hankali ta amsa tana dan lumshe idonta.

Kallonta yake yana ayyana abubuwa da yawa a kanta, yanayin ta ya nuna kamar mara lafiya.

Ya daure zuciyarsa yace." Ko kina da damuwa ne."?

Zuciyarta ta karye hawaye naso ya zubo tana mayar dashi bata bukatar tayi masa kuka tunda yana kiranta da shagwababbiya.

Shuru tayi ba tace masa komai ba. sai da ya sake maimata maganar sannan tace." Lafiya na kalau."

Ya kalli agogon dake daure a hannunsa da fadin" Okey haka nake so ni zan fita amma idan kinji wani guri nai miki ciwo ki kira ni a waya."

Ta kalleshi k'auna da sonsa na kara nunkuwa a zuciyarta, a jiyar zuciya ta sauke a hankali tace " To."

Ya kama hanyar fita jikinsa duk babu dadi, yarinyar ta tsaye masa a rai.

"Haka zaka fita ba kayi breakfast ba."?

Maganarta ta katse masa hanzari.  juyowa yayi yana kallonta.

Ta sunkuyar da kanta domin bata jurewa kallon kwayar idonsa.

" Kada ki damu zan samu abunda zan ci buri na ki tashi ki nemi abinci kici ko dan abunda ke cikin ki idan kinyi min haka kin gama min komai."

Ta yun'kura ta tashi tana d'an ya mutse fuskarta.

Saurin kawar da kansa yayi sakamakon ganin zahirinta kayan bacci ne a jikinta wanda suka fitar da wasu sassan na jikinta.

Yay gaggawar bude kofar dakin ya fita yana jin yanda jarumarsa ke motsi har ta fara yun'kuri! al'amarin ya bashi mamaki mutuka! koda yake ba'a abun mamaki bane idan anyi la'akari da kwanakin da ya dauka rabon da ya hada shinfida da ita.

Yana zama a ofis kiran wayar Maimartabar ya same shi.

Suka gaisa cikin mutunci da dattako.

Maimartaban yake sheda masa cewa suna da baki da misali sha biyu jirginsu zai sauka anan filin jirgi na Katsinan.

Farin ciki yayi sosai ya dinga godiya tare da adduar Allah ya saukesu lafiya.

Sukayi sallama cikin girmama juna.

Cike da farin ciki ya kira wayar ta.

Fitowarta daga wanka kenan tayi saurin dauka tare da zama gefan gado.

Ya sheda mata abunda yake faruwa.

Jikinta a sanyaye tace." Me yasa ka sheda musu abunda yake tsakanimu."? murya na rawa

take maganar

Yayi shuru yana nazarin maganarta.

Tace." Shikkenan na shiga uku  ka janyo min bacin ran iyaye na."

Ya kwantar da murya da fadin." Ni fa ban fada musu maganar da wata manufa ba, na fada musu ne domin su ta ya ni neman mafita, amma bana fatan ranar da zan shiga tsakaninki da iyayenki."

Ta share hawayen saman fuskarta  kawai ta kashe wayar saboda kukan da yake kokarin kufce mata.

Sake kiran wayar yayi tana kallo tana ringing taki dauka, ita yanzu tashin hankalinta zuwan Mahaifiyarta tasan bacin rai ne zai biyo ba.

Babu kuzari a tare da ita ta kimtsa jikinta, ta nemi kujera ta zauna tana duba agogo  sha biyu ta gota tasan yanzu mybe sun sauka .

Wayarta ta d'auka cike da fargaba ta kira mahaifiyarta.

Murya na rawa tace."Mommy ina wuni."?.

A dakile ta amsa gaisuwar.

Ta daure tace." Kun sauka ne."?

Gimbiyar tace." Eh sun sauka dan yanzu suka kira waya,  babu ni 'Yar uwata ce sai yayyunki."

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin sanyi a zuciyarta tasan SAFAH tana da sanyi rai ba kamar mahaifiyarta ba.

Ta katse tunaninta da fadin." Kin kyauta abunda ki kayi ZINA kin janyo min zagi da cin mutunci na gode." Ba ta jira amsarta ba, kawai ta kashe wayarta.

Ita kam shuru tayi da waya a hannunta  gabadaya ta rasa ya za tayi da rayuwarta.

SAFAH tare da Hassana da Hussaina da Magajin sarki suka sauka a gidan......Farin cikin ganinsu yasa ta fashe da kuka! ta dinga rungumesu duk ta rasa yanda za tayi saboda jin dadin ganinsu.

Magajin Sarki yace." Ki samu nutsuwa haka zuwan mu gidanki baya nufin farin cikin ki. akwai babban dalili ne ya kawo mu gidanki."

Ta nemi kan kujera ta zauna jikinta duk a sa'bule.

Ya fara yi mata fad'a tare da kawo mata ayoyin al'kur'ani da hadisai duk dai akan abunda ta aikata mara kyau!

Shuru tayi ba ta iya cewa komai ba, dukkaninsu kowa ya tofa albarkacin bakinsa mussaman SAFAH da ta dinga yi mata nasiha mai ratsa jiki anan ne ta zubar da hawaye, tana kukan tace." Mammah dan Allah ku gafarce ni wallahi tsautsayi ne da son zuciya insha Allah ba zan sake maimaita abu mai muni irin wannan ba.

Hassana tace." To Alhamdulillhi haka muke so muna rokon Allah ya sauke ki lafiya ya kuma inganta duk abunda zaki haifa."

Gabadaya suka amsa da "Ameen." Kafin su fara yun'kurin tafiya.

Tace." Mammah har zaku tafi ni wallahi na dauka kwana za kuyi."

Magajin Sarki ya harareta da fadin." Sai kace mahaukata ko."?

Ta 'bata rai da fadin." Aunty Hassana don Allah ku zauna ku kwana mana."

Hussaina tace." Baki da hankali ZINA daga zuwa sai mu kwana ke a ganinki hakan yayi dai-dai"?

Tace." To meye wallahi babu matsala kuna gani dai kowa da gurinsa to me zai dame ku."

SAFAH ta mike tsaye tana gyara yafan mayafinta da murmushi a fuskarta tace." Zinatu rigima kin ga tashi kiyi mana Jagora cikin gidan mu gaisa dasu. ke kanki kin san abinda kike bukata ba

mai yuwu wa bane.

Cike da rashin dadi ta tashi ta shiga daki domin dauko mayafi, nan Aunty Hussana ta bita dakin ta bata wata leda dake cike da turarukan wuta da humra masu kamshin gaske,  sai kuma kaninfari da yawa cikin wata leda a d'aure, tace mata ta jika cikin wani abu tana shan ruwan.

Godiya sosai tayi mata kafin su fito daga dakin a tare.

 Uwale tsohuwa mai dattako! ta kar'be su hannu biyu tana ina a saka ina a sauke dasu.......Da yake basa rabo da abinci ta sanya Hamra'u ta had'a musu abinci wanda zai gamsar dasu.

Haka nan suka saki jikinsu suka ci abinci wanda Hamra'u ta sarrafa sosai Allah yai mata baiwar iya sarrafa abinci ko wane iri ne a zahiri suma sun yaba sosai kuma ci sun gamsu.

Itama ZINAT din taji dadin yanda aka karramasu ta saki jikinta tamkar akwai sabo a tsakaninsu, har tana jan Hamra'un da hira, wanda hakan ya basu mamaki mutuka, to itama dai Hamra'un saki tayi kamar wani sa'bani bai  ta'ba shiga  tsakaninsu ba.

Tafiyarsu keda wuya ya kira wayarta yana tambayarta.

Tace." Ai har sun tafi."

Cike da mamaki yace." Sun tafi."?

Tace."Eh nima wallahi babu yanda banyi dasu ba su kwana amma sun tafi kamar ana korarsu."

Ya girgiza kai da rashin jin dadin hakan, yace." Me yasa da zasu tafi baki kira ni kin sheda min ba, sai  na bar duk abunda nake nazo mu gaisa."

Tayi shuru domin ba tasan me za tace ba.

Yace." Laifin duk naki ne Zina kwata-kwata banji dadin  tafiyarsu ba naso mun gaisa da juna sosai."

Tace." Kayi hakuri amma ai sun gaisa da Uwale har suka ci abinci a gurinta.

Yace." Hakan ma yayi amma Uwale daban ni daban."

Tace." Hakane kuma." Shuru ya ratsa tsakaninsu kafin tace." Daddare me kake bukatar ci."?

Kai tsaye yace." Towon dawa da miyar kuka."
Iya gaskiyar sa ya fadi maganar.

Amma sai ta kyalkyale da dariya da fadin." Towon dawa! gaskiya ni ban iya ba."

Yace." Aikuwa ki koya domin shine favorite d'ina mussaman dumame towo ko wane iri ne ina sonsa.

Tace." To shikkenan kada ka damu yau ma da kaina zan maka abincin insha Allah."

Yace."Okey da can bake kike ba kenan."?

Da sauri ta gyara maganarta tace." Ni ce mana ina nufin yau na mussaman zanyi maka towon da kake so.

Yace." Idan da akwai matsala ki zauna ki huta kin san baki da koshin lafiya."

Murmushi tayi da fadin." Naji sauki ai ina bukatar samun ladan aure."

Murmushi jin dadi yayi yana juyi kan kujerarsa yace." Shikkenan yau da daddare za muyi hira kenan."

Tana 'yar dariya tace." Sosai irin wacce ba mu ta'ba yin irinta ba."

Yace." Alhamdulillhi na gode Allah da ya bani ke a matsayin matata."

Tace." Nima haka amma dai ka yafe min laifi na ko."?

Ya gyara zamansa da fadin." Na yafe miki kuma da ikon Allah zan d'aga miki ki shiga aljanna Bakya laifi a guri na GIMBIYATA."

Tace." Na gode *Mazan Fama!* Allah ya barmu tare." ya amsa da "Ameen wani irin farin ciki na ziyartarsa.

Aikuwa kamar yanda tayi masa alkawari, da kanta ta shiga kicin din, ta sanya Marakisiyya ta harhad'a mata komai wanda zata bukata, yau abunda bata ta'ba yi ba zata kwatanta.

Ita kad'ai a kicin din tana gwagwarmaya! duk ta jigata, sai gumi take abunka da wanda bai saba ba.

Akayi rud'e kalau! aka rufe ruf! sannan aka shiga had'a miya, tayi dubarar silala naman da albasa da kayan 'kamshi amma bai wani dahu sosai ba, ta zuba su daddawa da kayan miyan data murza a gireta, ta zuba uban farin mai tamkar me shirin yin jar miya.........Can rud'en dake rufe ya fara za'bal'bala kafin kice me murfin tukunyar yayo sama talgen ya fara kumfa yana zuba saman gas din, da sauri take k'okarin cire murfin aikuwa ta 'kone a hannu!! baya ta matsa tana ihu!! taje ta kwance famfo tana wanke talgen daya kona ta. kuka ne kawai ba tayi ba fatar hannunta tayi jajawur! ido jawur! ta fita daga kicin.

Ta zauna kan kujera tana mayar da numfashi..........A'a abu kamar wasa hannu ya fara tashi! ga wani irin zafi da yake mata......kira ta kwalawa Marakisiyya tace mata maza taje ta k'arasa ita tayi abunda zata iya.

Tashi tayi ta shiga d'aki ta kwanta, tana jinyar hannunta.

Daf da zai shigo gidan ya kira wayarta, ta daga su gaisa yana tambayarta jikinta, tace." Lafiya amma garin yi maka towo na k'ona hannu.

Yace." Subahanallahi garin ya hakan ya faru."?

A shagwabe tace." Talgen ne ya dinga zuba naje bude tukunya ya zubo min a hannu."

Yaji duk wani iri a jikinsa yace." Sannu my love amma ba sosai bane ko."?

Tace."Eh ba sosai ba amma har ya tashi sai ciwo yake min."

Yace." Yi hakuri kinji bari yanzu zanzo nai miki addua insha zaki ji sauki."

A sanyaye tace." Okey my darling na gode sai ka shigo." kashe wayar yayi yana Allah-Allah ya isa gidan.

Wanka tayi ta kimtsa domin bata so ya shigo ya sameta babu ado, tunda tasan yana san haka

shiyasa ta mayar da hankali gurin yi masa ado da kwalliya na kece raini.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: *Assalamu alaikum warahmatullahi masoya yan uwa na musulmai...*
🐫🐫🐫🐫🐫
🐫🐫🐫🐫
🐫🐫🐫
🐫🐫
🐫
*Tabbas wani kaya sai amali ,busa sai sarewa jiniya sai a gidan gomna ,ina kuke mata ma'abota tambayar ina wannan shahararriyar y'ar mutan nijer wato mali ,wacce akafi ma lak'abi da...*```🐫BUZHUWA EMPIRE🐫```
*Ina kuke matan Aure n mu masu fuskantar tangard'a tare da k'alubale a gidan mazajen Auren mu??💃💃.*
*Ina kuma y'ammata masu buk'atar farin jini ta hanyar samun mijin Aure?? Don raya sunnar manzon mu SAW...Nasan duk kunce gamuuu!!!👆👆👆.* *Gafa BUZHUWA EMPIRE ta* *taho maku duk don share hawayen dake kwaranya akan fuskokin ku ta hanyar kawo maku sirrin mallaka tare da* *magani ,haka ma y'ammata ga sirrika nan da maganin shi ,wanda anyi mutane babu adadi kuma anzo anyi* *godiya....ki tambaya wacece Buzhuwa empire ga dukkan wanda* *yasanta ,zakuji karin bayani daganan. Muna bada mallaka ta hanyayoyi dabam* *dabam ,wanda da alfarman annabin rahma xamu sha mmki.* *Mallakar tamu akwai na 3k akwai na 5k ,akwai na 10k da sama ma da haka. Mudai fatan mu shine babu cuta babu cutarwa , kamun mu biya* *maki bukatanki sai kin mana rantsuwa akan bazaki cutar dakowa* *ba ,mallaka matan aure muke ba zallah. Na farin jini kuma na y'ammata ne ,shi munayin shi akan 5k ne da kuma na 10k.* *Zakuna iya tuntu6an wannan numbern domun karin bayani...09061466409/08081202932.*
*Ga kad'an daga cikin mallakar da muke amfani wajen yinsu👇.*
*Mallaka ta hanyar K'wai.*
*Mallaka ta hanyar nono*
*Mallaka ta hanyar zobe*
*Mallaka ta hanyar guru*
*Mallaka ta hanyar turaruka da dai sauran su.... Sai kin taho domun share hawayenki daga kunci zuwa farin ciki....* ```BUZHUWA EMPIRE taku ce!!!```
~08081202932 ko 09061466409~

*95&96*
Cikin shirin bacci ya sameta zaune a bakin gado ta zabga tagumi! fuskar nan a had'e! da alama jiran kiris take ta fashe da kuka! ya 'karasa ya zauna kusa da ita tare da kiran sunanta, bata amsa ba sai ma janye jikinta da tayi, hakan beyi masa dadi ba, amma sai ya daure tunda hakan ba sabon abu bane a gurinsa.

Hannunta ya laluba ya rike cikin nashi murya a tausashe yace."Me yake damunki."?

Kawai sai hawaye ya fara zuba a saman fuskarta!

Ya zuba mata ido yana mamakin kukan da take, shi dai yana kokarin kiyaye abinda zai had'asu rigima ko wani tashin hankali, burinsa a yanzu bai wuce ace ta kwantar da hankalinta ba dan ingantuwar lafiyarta.

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke ya janyota jikinsa yana rarrashinta bai kuma fasa tambayarta damuwarta ba.

Ta cire jikinta daga jikinsa tana share hawaye! tace." Nifa ban shirya haihuwa yanzu ba."

Gabansa yana faduwa yace." Bangane abunda kike nufi ba."

Tayi kokarin hadiye yawun bakinta kafin ta sake maimaimata masa maganarta.

Yasha mur! kamar bai ta'ba dariya ba yace." Okey to da baki shirya haihuwa yanzu ba ya kike so ayi? kin san dai rayuwar kaf ba a hannuki take ba ballanatana kice za kiyi yanda kike so. Shin meye ribar aure."?

Shuru tai masa ba tace uffan ba.

Ya sake maimaita maganarsa...."Ki bani amsa nace meye ribar aure."?

Tayi 'kasa da kanta tana wasa da yatsun hannunta.

Murmushi takaici yayi ya girgiza kai tare da fadin." Kiyi hakuri ki bar wa Allah ikonsa kada ki butulce masa mutane da yawa suna can suna nema ido rufe bai basu ba, amma ke ya fifitaki a kansu yayi miki kyauta mai muhimmanci amma ki nuna bakya muradi kada kiyi haka, kawai kiyi addua Allah ya saukeki lafiya yasa kuma abunda zaki haifa cikon addinin musulunci ne."

Duk wannan maganganun da yake bai sa ta saduda ba kawai dai tana jinsa ne amma ba zata janye kud'irinta ba.

Ya dinga kwantar da murya yana rarrashinta da kalamai masu sanyi duk a tunaninsa shurun da tayi tana d'aukar nasiharsa,  sai dai kuma washe garin ranar yana fita gurin aiki ba da jimawa ba kiran wayar gaggawa ya sameshi cewa yazo gida babu lafiya.

Magashiyan! ya sameta a kwance tana murkususu! cikinta ya d'aure sai wani mugun ciwo yake mata gabadaya ta fice daga hayyacinta!.

emagency suka nufa cikin gaggawa  aka bata taimakon gaggawa! anan likitan ya gane lallai tasha wani abun domin yunkurin zubar da cikin jikinta.

Wannan bayananin yayi masa yana kara jadadda masa da cewa lallai ya sanya ido ya kuma kula da kyau domin dai cikin ya kai matakin da idan akace dole sai an zubar dashi za'a samu matsala.

Hankalinsa ya tashi ainun!  gabadaya ma ya rasa wane irin tunani zai yi, ashe kiyayyar da take masa har ta kai haka.

Koda suka koma gida bece mata komai ba sai da ya tabbatar da cewa taci abinci tasha magani sannan ya koma gurin aiki tare da tunanin matakin da zai dauka.

Sai da ya dan samu nutsuwa tukkuna ya lalubi number mahaifinta gwara ya shedawa iyayenta abunda yake faruwa kada ta kashe kanta suga laifinsa.

Cikin mutumci da mutuntawa suka gaisa da juna Maimartabar ya dinga yi masa addua tare da cigaba da samun kwanciyar hankali da zaman lafiya..

Jikinsa ya mutu! ya dinga tunanin yanda za'ayi ya sheda masa abunda yake faruwa, mutumin nada kirki sosai kuma baya so ya tayar masa da hankali domin duk uban da yaji cewa ga abinda 'yarsa keyi a gidan aure dole hankalinsa ya tashi, amma ya zama dole ya sheda masa

domin hakan shine mafita.

Iyakar abinda ta aikata a yau din ya sheda masa  amma ya boye sauran laifukan da take masa! a ganinsa duk basu kai matakin da zai kai 'karar ta a kansu ba.

Maimartaba yayi shuru yana jimanta al'amarin...... sai ya shiga tunanin abinda ya shud'e!.

Danne 'bacin ransa yayi kafin ya shiga bawa UMAR din hakuri  tare da fadin ya cigaba da kai zuciyarsa nesa a kan yarinyar yana kawar da kansa kuma ya cigaba dayi mata adduar shiriya insha Allah komai zai wuce, shima kuma a matsayinsa na mahaifinta zai dauki mataki akan abunda ta aikata.

Suka rabu cikin mutunci tare da jajantawa juna koba komai ta tayar da hankalin iyayenta domin a ranar Gimbiya Aysha kasa rintsawa tayi abu biyu suka dameta  bakin cikin abinda 'yar ta keyi sai kuma tashin hankalin da mijinta yayi mata a cewarsa duk abunda ZINATU keyi abunda ta aikata ne a baya tarihi yake maimaita kansa,  ta tsani wannan kalmar tana fitowa daga bakinsa.

Bai shedawa Asp abunda yake faruwa ba, sai da suka had'u gaba da gaba domin maganar ba zata yuwu a waya ba.

Shima Asp din lokacin da yaji maganar ya girgiza ya dinga nanatawa yana al'ajabin al'amarin.........Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Yanzu ya jikin nata."?

Yace."Da sauki alhamdulillhi kuma likita ya tabbatar da cikin yana nan bai fita ba, amma ni har yanxu ban sanya raina a kansa ba, ina ganin za ta iya bin wata hanyar ta zubar dashi.

Yace." Insha Allah hakan ba zata faru ba,  sannan kuma idan ba damuwa inaso kayi min jagora zuwa gareta."

Kai kawai ya daga masa yayi gaba sai ya rufa masa baya dukkaninsu zuciyarsu babu dadi.

Shi ya fara shiga ya sheda mata zuwan Asp din ba tare daya jirayi amsar ta ba ya fito daga dakin dan bala'in shaushinta yake.

Ta fito cikin dogon hijab kamar wata mutuniyar arziki, saboda tasan bata da gaskiya har kasa ta durkusa tana gaisheshi bai kai ga amsawa ba kawai ta fashe masa da kuka!

Ido kawai ya tsira mata  tausayi yarinyar take bashi ya dinga raya wani abu a cikin zuciyarsa, wani sa'in idan mutum na aikata abubuwa marasa kyau! da akwai hali amma kuma akwai sanya hannun aljanu a ciki.

Ganinta tana kuka  yaja tsaki ya kama hanya ya fita a ganinsa ba ita ya dace tayi kuka ba, shine kuka ya dace dashi duba irin wasiwahsin da ta jefa rayuwarsa a ciki.

Asp din ya bishi da kallo yana gyada kansa, sam bai ga laifin abunda yake ba, domin an shiga huruminsa

Ya kalleta tana ta aikin share hawaye wasu na zuba, ita kanta tasan abunda tayi ba daidai bane to za'a tayi da zuciyarta gaskiya ita ba taso ta haihu ta tsufa da wuri shiyasa tayi yunkurin zubar da cikin tun beyi kwari ba, ashe tana da rabon shan wahala! domin ita kadai tasan irin bakar wuyar da taci sakamakon abinda ta aikata.

Yace." Zinatu abinda ki ka aikata ya sa'bawa shari'a kin aikata mummunan laifi irin wanda Allah baya so,  yanzu da Allah ya dauki rayuwarki sanadin zubar da cikin halak me za kije kice masa."?

Wasu hawaye masu zafi suke sake wanke mata fuska, sai kawai jikinta ya shiga karkarwa!

Ya cigaba da cewa. Kiyi istigifari ki roki Allah gafara akan abinda kika aikata Allah gafurur rahimu ne zai yafe miki sai abu na gaba ki nemi afuwar mijinki! sannan kuma kada ki sake yunkurin aikata mummunan aiki irin wannan! wannan ce kawai shawarar da zan iya baki."

Kasa cewa komai tayi kawai kuka take tana girgiza kai tare da istigifari a cikin zuciyarta.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ki daina kuka bashi ne mafita ba. kukan zai iya janyo miki wata

matsala.

Da kyar ta iya bude baki tace." Na gode sosai Ranka ya dade insha Allah ba zan sake ba.

Yace." Allah yasa Allah kuma ya yafe miki kuskuranki." Ta amsa da "Ameen tana kokarin tsayar da ruwan hawayen dake zuba.

Abokin nasa ya kira yace yazo shi zai tafi......minti biyar sai gashi har yayi wanka ya sauya kaya bakar jallabiya mai karamin hannu da botira  kansa sanye da hula tashi ka fiye naci.

Ya kalleshi da fadin." Naga kasa hula sai kace wani balarabe fita za kayi ne."?

Kansa ya girgiza tare da kokarin zama a kusa dashi yace." Babu in da zani.

Yace." Okey ga tanan tayi nadama kuma tace na taya ta baka hakuri, kasan  dan Adam  ajizi ne kowa yana kuskure don Allah ka yafe mata."

Shuru yay bece komai ba  ya tsirawa tv ido haka kawai baya son kallon fuskarta.

Ganin yayi shuru beyi magana ba, yasa Asp din duba agogon hannunsa tara shaura na dare, ya mike da fadin." Ni zan shiga gida Allah ya kiyaye gaba."

Ya kalleshi da fadin." Ameen ya Allah na gode sosai Allah ya saka da alkairi a gaishe min da Daughter."

'Yar dariya yayi  tare da jin dadin yanda yake nuna kauna da kulawa a kan 'yarsa  yace." Nabila za taji da kyau insha Allah."

Bayan fitar Asp din da minti biyu ta kalleshi gabadaya hankalinsa nakan tv kamar bai san da ita a gurin ba.

A sanyaye taje ta zauna kujerar da yake zaune da yake 1sitar ce sai suka takura jikinsu ya hadu sosai.

Bai kalleta ba ballanatana ya tanka mata still bai janye idonsa daga abinda yake kallo a tv ba.

Sajen dake kawace da fuskarsa ta fara wasa dashi ta dora kanta saman kafadarsa, murya na rawa tace." Kayi hakuri don Allah."

Sanyi yaji a zuciyarsa amma bai nuna a zahiri ba,  ya janye jikinsa kanta ya sauka  daga kafadar ta sake mayarwa wannan karon gabadaya ta zuba hannayenta a cinyarsa.

Kallonta yayi babu walwala a tare dashi yace." Wane magani ki kasha."?

Shuru tayi tana sauke ajiyar zuciya nauyi da kunya ya hana ta magana.

A fusace! yace." Ko bakya ji ne."?

Ta kalleshi ruwan hawaye na kokarin zuba tace." Bafa magani nasha ba ka daina min tsawa! ka kyaleni naji abunda ya dameni."

Ya sake tuge kafadarsa kanta ya sauka a karo na biyu, kallon ido da ido yayi mata kafin yace." Zaki k'aryata maganar Likita kenan."?

Kasa had'a ido tayi dashi saboda kunya.

Yace." Ki fada min maganin da kika sha domin salwantar min da gudan jinana.

Hannu tasa ta share gumin saman hancinta sai  ta fara inda-inda........."Bafa magani bane gish.......Ta kasa karasa maganar sai shine ya 'karasa da fadin." *Gishiri!"?* kai ta daga alamun "Eh."

Ya dinga girgiza kansa yana mata kallon mamaki kafin yace." Ya akayi kika san gishiri yana zubar da ciki  ko dama can kin ta'ba zubarwa."? yana sane yayi mata wannan tambayar.

Aikuwa ta kad'u!  ta zuba masa ido tana masa wani irin kallo,  maganar kawai take maimatawa a zuciyarta *"Ko dama  can kin ta'ba zubarwa."?* shin me yake nufi?

Wasu zafafan hawaye masu azaba suka fara sauka asaman fuskarta  sam ta kasa tsayar dasu saboda zubarsu ne kwanciyar hankalinta

Ya kalleta sam bata bashi tausayi ba, saboda duk sanda zai kalli fuskarta sai ya tuna ta'addancin da take kokarin yi masa.

Ya sha mur!  babu fara'a yace." Ke shagwabbiya ko? daga anyi magana sai ki bude baki kina kuka   alhalin kice baki da gaskiya to ba kuka nace kiyi min ba cikakken bayani zaki min."

Tayi  namijin kokarin had'iye kukan ta share fuskarta, zuciyarta na wani irin tafarfasa! tace." Kace nayi abortion ko."?

Ya girgiza kai da fadin " Aa ni tambayarki nayi amsa zaki bani.

Ta had'iye wani kuttun takaici kafin tace." Kai zaka shedawa jama'a cewa ga  yanda ka same ni dan haka bani da lokacin yi maka bayani."

Tana gama maganarta ta tashi ta bashi guri. zuciyarta kamar ta fashe saboda bacin rai.

Tabbas da ta san irin zargin da zai biyo baya kenan to da ba ta dauki shawarar Sakina ba domin tun farkon faruwar al'amarin tayi shawara da ita kuma itace ta tabbatar mata da cewa gishiri yana zubar da ciki *Subahanallahi! ciki ko na haram ne ba'a san zubar dashi, ballanatana na halak!  dan haka a kiyaye dan Allah abi dokar Allah dan a samu zaman lafiya.*

*Ayi min afuwa banyi posting akan lokaci ba muna matsalar wutar NEPA ne  NAGODE🙏🏻*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*99&100*
Wani sanyi ne ya ziyarceshi yayin da yayi tozali da ita a hakimce tayi ado irin wanda yake bala'in burgeshi, in  ban da kamshi babu abunda take........Gabadaya wata irin kasala ta rufeshi tsananin sha'awarta ya sake kamashi,  shi dai yana bala'in son kamshin jikinta.

Kusa da ita ya zauna ya jifanta da wani irin kallo, ta marairace fuska tana kallonsa kafin tayi masa barka da zuwa.

Ya dubi hannun da ya kone!  tsigar jikinsa ta tashi, a hankali ya rike hannun ya fara tofa mata addua  ya gama ya kalleta cike da kulawa yace." Ke zanyi wa sannu  duba da irin tsautsayin da kika samu ta dalili na,  tunda kika sheda min hankalina ya tashi ina Allah-Allah na iso gida naga halin da kike ciki, amma abun mamaki sai na sameki cikin koshin lafiya kinyi ado da kwalliya irin wanda nakeso ina mai tabbatar miki da cewar ina alfaharin kasancerki a matsayin matata."

Murmushi tayi tare da jin dadin kalamansa, dama kuma babban burinta bai wuce ace ta siye zuciyarsa kaf ya daina ganin ko wace mace a gabansa ba sai ita, ta lura yana da sau'kin kai! kuma ta fahimci ya kamu da tsananin sonta wannan abin alfahari ne a gurinta.

*****
Da safe kafin ya fita gurin aiki yake sheda mata tafiyar da za suyi, sam ba tayi tunanin cewa har da ita za'ayi tafiyar ba, sai da taji yana fadin." Za ku kwana biyu a k'auyen  domin kisan 'yan uwana suma su sheda ki sosa."

Sai ta kasa 'boye bacin ranta!   ta dan 'bata fuska tana kallonsa.

Ya fuskanci ba tayi na'am da tafiyar ba,  ransa bai masa dadi ba.

Ganin taki yin magana ya sanya ya tashi da niyyar fita.

Ta kalleshi a lokacin da yake gyara f-cap din kansa.  da kyar tace." Sai ka dawo."

A dakile ya amsa ya kama hanyar fita zuciyarsa duk babu dadi, sam bai ji dadin abinda tai masa ba, ya lura har yanzu ba ta k'aunar a halinsa, a ganinsa duk soyayyar da take nuna masa a banza take, mutukar ba zata kaunaci yan uwansa ba.

Ya saba kiran wayarta idan ya samu saukin aiki amma a ranar sai ya share ta  yana so ya nuna mata kuskuranta

B'angaranta kuwa ba wai zuwa 'kauyen ne ba taso ba,cewar da yayi zata zauna tare dasu har na tsayin wasu kwanaki shine abinda ya 'bata mata rai! gaskiya bata tunanin kwana a kauyen 'kafarta-'kafarsa.

Da taji shuru bai kira ta ba, sai ta kira shi, ya daga yana shan k'amshi.

Murmushi tayi kafin tace." Fushi kake ko darling."

Gyaran murya kafin yace." Fushi akan me? a halinki ai ba sabo bane a gurina."

A shagwabe tace." Au! mugun hali ne dani."?

Yayi shuru bai ce mata komai ba.

Ajiyar zuciya ta sauke a sanyaye tace." Kayi hakuri ba wai bana so naje bane naji kayi maganar kwanaki shine bana so."

Ya fusata!  yace." Kin ga idan ma ba zakije ba kiyi zamanki okey." Kawai ya kashe wayarsa.

Ta dinga bin wayar da kallon mamaki! ita fa yanzu kwata-kwata bata bukatar abunda zai shiga tsakaninsu, amma ta fahimci akan 'yan uwansa zai iya cin mutuncin kowa.

A'a! abu kamar wasa 'karamar magana na nema ta zama babba!  fushi yake da ita sosai! dan koda ya dawo daga gurin aikin bai shiga gurinta ba, ya gama duk abunda yake ya nufi sashensu Uwale, zuciyarsa duk babu dadi.

Koda taji shuru bai shigo ba, sai ta yanke shawarar   zuwa gurinsa, tunda zuwa yanzu ta san ya dawo, ita sam ba taga abun fushi da 'bacin rai ba,  bata gudin 'yan uwansa. halinsu ne kawai abun gudu.

Koda ta shiga gurin nasa,  Babu shi babu dalilinsa.  amma akwai alamun ya dawo yayi wanka sannan ga 'karamar wayarsa nan a saman drowar.

Kai tsaye gurinsu  Uwale ta nufa domin tana da tabbacin  yana can.

Abunda taci karo dashi ya kusa tarwatsa mata zuciya, amma sai ta jajurce! tayi kokarin danne mugun kishin da yake taso mata.. tayi musu sallama.

Su biyu ne a falon, Uwale na daki domin gabatar da sallar magariba, shima dawowarsa kenan daga massalancin, ya samu Hamra'un ta shirya masa lafiyayyan towon farar shinkafa da miyar kubewa d'anya wacce taji bushashshen kifi da man shanu!

Ya dinga shi mata albarka domin yini cur bai ci abinci ba, tun breakfast din safe, b'acin ran da ya fita dashi ya ha nashi cin wani abu.

Tana zaune durshan a gabansa bayan ta zuba masa abincin yana ci tana bashi labarai sai dariya yake sai kace mata da miji.

A zabure! ta kalli bakin kofar! suka had'a ido, bahaushe yace (Mara gaskiya ko a ruwa gumi yake) duk sai ta daburce! tayi gaggawar matsawa daga kusa dashi, shi kam ko gezau! abincinsa kawai yake ci amma ya amsa sallamar bai dai kalleta ba.

Ta zauna kujarar dake kallonsa da fadin." Ranka ya dade ashe ka dawo."?

Ya dago kansa yana kallonta da mamakin sunansa da ta kira shi, sam bai mayi tunanin za tayi masa magana ba, saboda ya san azabar kishinta.

Da yake Namijin duniya ne babu kunya yace." Eh na dawo kina raina yanzu nake maganarki a zuciyata."

Taji kamar ta fada masa bakar magana! amma sai tayi shuru kawai tana masa wani irin kallo na tuhuma!

Saurin sunkuyar da kansa yayi! duk dadin towon a bakinsa yaji ya fice masa daga rai!

Hamra'u kam! simi-simi ta kama hanyar d'akinta! tana ta wani kumbura fuska shigowar Gimbiyar ya 'bata mata rai mutu'ka! domin ta katse mata jin dad'inta.

Ya kalleta da fadin." Ya zaki tafi baku gaisa ba.

Ya'ke  tayi ta juya da fadin." Aunty Gimbiya ina wuni."?

Tace." Lafiya lou ina Uwale."?  Kafin ma ta bata amsa Uwalen ta fito da carbi a hannunta,  ganin Gimbiyar yasa ta washe bakinta, sosai tayi farin cikin ganinta a zaune  babban burin ta ace Gimbiyar ta saki jikinta dasu.

 Hamra'u kasa tsayuwa tayi a gurin da sauri ta shige dakinta, ranta idan yayi dubu ya ba'ci, ita dai tana kishin yanda Uwale ke nuna kauna da kulawa akan Gimbiyar.

Cikin mutuncin da girmamawa suka gaisa da juna.

Ta kalleta da fadin." Ya jikin naki jiya Ai yake fada min kin 'kone a hannu har nake cewa zan shiga na dubaki Allah bai bani iko ba."

Tace." Ai ba sosai na k'one ba, kuma tunda yayi min addua gurin ya bushe ya daina ma zafi."

Tace." Duk da haka dai ai kin tsallake tsautsayi! kin ma yi kokari abunda ba ka saba a kansa ba, ai dole ka sha wahala."

Murmushi tayi amma ba tace komai ba.

Da farin ciki a maganarta tace." Mijinki ya sheda miki gobe za muje 'kauye ko "?

Fuska a sake ta amsa " Eh ya fad'a min Allah ya nuna mana goben lafiya."

Tace." Ameen  ai yana da kyau kema ki saba da dangi shiyasa da yace shi ba zai kwana ba, nace to ya zama dole ke ya barki tare damu domin 'yan uwa su sheda fuskarki ai riga an zama d'aya."

Tace." Hakan yayi insha babu matsala ta b'angare na,  ina tare daku."

Kallonta yayi yana mamakin furuncinta.

D'auke kanta tayi dan tunda suke maganarsu bata kalleshi ba saboda masifar haushinsa da

take ji.

Uwale sarkin hira da labarai na ban dariya ta dinga bata labarai irin na da! ta dinga dariya tana mamakin kokari irin na mutan da! ace Mace ta haihu amma unguwar zoma ta fita yawan nama! ita abun ma dariya ya dinga bata.

Ganin kamar sun manta dashi a gurin yasa ya tashi domin zuwa ya kwanta a gajiya yake tilis!

Ta kalleshi da fadin." Ya zaka tashi kuma."?

Yace." Eh mana to zaman me zanyi kun manta dani kuna hira bakwa sani a ciki zanje na kwanta ne."

Dariya tayi irin ta tsaffi! kafin tace." To ai gwara ka kwanta ko ka tashi da wuri nima nafiso muyi sammako."

Yana kokarin fita yace." Uwale ai ke yau bana tsammanin zaki iya bacci ."

Ta fashe da dariya da fadin." Me zai hana zanyi wanda ya sawwa'ka dai ai dole nayi zumudi UMARU wata da watanni ba tare da 'yan uwa ba." Da al'ajabi ta k'arasa maganar.

Girgiza kansa kawai yayi kafin yace." Sai da safe kenan ya kalleta bata da niyyar tashi su tafi......."A nan zaki kwana ne."?
Ya jefa mata tambayar hannunsa na rike da handle domin bude kofar.

A nutse ta mik'e ta kalli Uwalen da fadin." Sai Allah ya kaimu." Ta amsa da "To Allah ya tashe mu lafiya Alla ya bamu alkairi."
Kusan a tare suka amsa kafin ya bude kofar ya fita ta bi bayansa.

Kowa sashensa ya nufa, bata tsammanin bin sa domin yanda zuciyarta take a tunzure! bata tsammanin
zasu wanye lafiya. munufiki ne har yanzu akwai abunda yake 'boye mata.

Wanka tayi ta sanya kayan bacci tayi kwanciyarta tana tunanin irin hukuncin da za tayi masa

cikin ruwan sanyi, abu d'aya za  tai masa ya shiga damuwa! shine ta hana shi kanta wannan shine babban tashin hankalinsa, tabbas zai kawo kansa anan za ta fanshe in yaso yaje gurin yarinyar ta bashi kanta, tunda yana zuwa yaci abincinta a boye.

Washe gari da wuri ta  gama shirinta sosai ta had'a musu tsaraba cikin baggo,  sai da ta shirya tsaf sannan ta zauna domin karyawa.

Lokacin ya shigao cikin farar shadda kar!  wando da  riga iya gwiwa da wani irin tsadaddan aiki a wuyan rigar da hannu.  yayi kyau sosai rashin sanya hula shine yai masa cikas, da alama bashi da ra'ayi ta sosai.

Ta kalleshi ta 'kara kallo, yana da kyau sosai sai yanzu take tantancewa dole mata su rikice a kansa, itama tana masifar sonsa saboda yana da baiwar da ba kowane namiji ne ke dashi ba.

Abinda take rayawa a kansa shima irinsa ne a zuciyarsa,  duk kwanan duniya  'kara sonta da kaunarta yake a zuciyarsa.

Sanyayyar ajiyar zuciya ta sauke kafin ta gaishe shi a sanyaye.

Babu yabo babu fallasa ya amsa yana gyara agogon sarkar dake hannunsa, yace." Har kin shirya kenan."?

Shuru tai masa bata ce komai ba. ta cigaba da kurbar tea din dake gabanta.

Saboda neman magana sai ya kai hannu yana so ya dauke cup din.

Ta kalleshi  da fadin." Ya haka kuma."?

Yace." So nake na sha."

Murmushi kawai tayi ta sakar masa cup din.....ya dauka ya kai bakinsa dai-dai bakinta ya shanye tas!

Ta yunk'ura ta tashi daga gurin.

Ya bi bayanta da kallo a lokacin da take kokarin shiga dakin, yawu ya had'iye ya lumshe idonsa! bayanta kad'ai ya isa ya gigita duk wani namiji lafiyayya dama mara lafiya.

Bayanta yabi jikinsa duk yayi la'asar!  ya same ta tana kokarin nad'a lifaya a jikinta.

Yaje gurin da fadin." Bakya jin zafi zaki nad'a wannan bayan kayan dake jikinki." Yana maganar yana ha nata abunda take.

Ta kalleshi da fadin." Zafi kuma."?

Kansa ya daga da fadin."Eh ana zafi a gari ko bakya jinsa ne."?

Ta san neman magana yake da ita kawai sai ta cire lifayar ta ajiye,  hijab ta d'auko amma bece komai ba. sai abun ya bata mamaki ganinta kamar a yanzu zai magana tunda a zahiri kamar hijab din zai fi lifayar zafi, amma bece komai ba sai aukin kallonta yake gabadaya kwayar idonsa ta sauya!  ganin haka yasa da sauri ta kama hanyar fita tare da fadin." Wannan jakar baggo din ka fito da ita kaya ne a ciki."

Da hannu ta nuna masa, yabi gurin da kallo kafin ma yayi magana  ta fita daga dakin.  Zazzafar ajiyar zuciya sauke  kafin yasa hannu ya dauki bakkon ya bi bayan ta   da tunanin wani abu a ransa.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita  kukan ki ya kare_

*GJSR*

*101&102*
Itace a kusa dashi, Uwale da Hamra'u kuma a baya a tsakaninsu suke hirar da ta shafe su, ita dai tayi shuru tana dai jinsu, gabadaya tunaninta ya ta'allaka ne gurin ganin yanda za ta koyi mu'amula da 'yan uwansa, a jikinta takejin kamar akwai abunda zai faru sakamakon zuwanta garin.

Shi tunaninsa yasha bam-bam da wanda takeyi, domin shi kadai ya san halin damuwar da yake ciki a halin yanzu sha'awa ce tafi damunsa, gashi yayi wa Uwale alkawari yana ganin da kamar wuya alkawarin nan ya tabbata domin tare da matarsa zai tafi, saboda samun saukin abinda ke damunsa.

Daga karshe dai shuru yayi musu ya daina sanya musu baki a hirar sai ya kasance su biyu kadai suke magana a motar yanayinsu ya nuna d'okin kasancewa da 'yan uwansu.

Daf da za su shiga garin ya kalleta, yaga duk tayi wani iri sai ya mutse fuska take, da alama akwai abunda ke damunta ta dai yi shuru ne kawai.

Sassauta murya yayi da fadin." Menene."?

Kallonshi tayi da gajiyayyun idanuwanta tace." Zuciyata ce take tashi!.

Yace." Saboda me."? shuru tai masa tana ganin ko ta fada masa dalili bai zama lallai ya yarda ba."

Yace." Ba zaki magana ba."?

Ta sauke ajiyar zuciya mai sanyi kafin tace." mybe tafiyar mota ne." Ta dan ja tsaki mtssw! kafin ta cigaba da cewa ."idan ba yau ba din ba, bana tsammanin na ta'ba dogowar tafiya a mota irin wannan."

Yayi shuru yana nazarin maganarta, kwarai hakan na iya faruwa idan anyi la'akari da irin gidan da ta fito mostly masu kud'in nan ba sa jurar tafiyar mota 'karamar tafiya sai hau mata jirgi.

Yace."Sannu ai mun shigo garin da ikon Allah."

Ba tace masa komai ba kawai ta jingina kanta jikin kujera tana sauke numfashi sannu a hankali.

Uwale ce ta iya tofa albarkacin bakinta a kan maganar amma Hamra'u ta tafas! ba tace ba, sai wani dauke kai take tana kumbura fuska.

Tunda suka shiga garin motar ta fara gargada tana ciccijewa sakamakon kwazazzabai da

ramuka!  bayan wannan yara da almajirai suka dinga bin motar da gudu suna ihu!!!!!!!

Al'amarin ya daure mata kai mutu'ka! ashe lalacewar 'kauyen har ta kai haka?  ko'ina ginin jar kasa da wasu dirka-dirka bishiyon kuka da tsamiya had'e da mangaro gasu nan dai iri-iri!  garin cike da dabbobi barkatai yaransu da manyansu cikin 'kazanta abun dai sai godiyar Allah.

Uwale sai wangale Baki take tana d'agawa yaran dake bin motar hannu, a tunaninta suna ganinta motar tintac ce ita take ganinsu amma su basa ganin na ciki, su dai farin cikinsu mota ta shigo garin.

Can  wani fili mai yalwa ya nufa domin gyara parking.....Lokacin gungun!  yaransa suka durfafo gurin suna bushe-bushe karnukan dake biye dasu na haushi gurin ya kacame! 'kura sai tashi take!

Hankalinta ya tashi ganin haukan da yaran nasa suke! saboda haka yana gyara parking din ta kalleshi lokacin jikinsa har ya fara tsuma! gumi na karyo masa! tace." Dan Allah kada ka biye musu ina nufin kada kayi wannnan abun da kake bana so."

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke ya ciro hankici daga jikinsa gumin fuskarsa ya goge  kafin ya juya gurinsu Uwale lokacin tana ta kici-kicin bude kofar motar.

Ya mika hannu ya bude musu kofar suka fita........Karnukan suna hangoshi a motar sai suka sake rikicewa! da haushi kokari suke iske in da yake, ta rintse idonta da karfi tace." Kada bari su shigo ka rufe motar.

Gaggawar rufewa yayi yana kallonta jikinta sai karkarwa yake,  'kwalla ta cika kwarmin idonta, yana daya daga cikin dalilan da yasa bata kaunar zuwa k'auyen! ta tsani ta bude ido tayi tozali da k'azaman karnukan da idanuwansu ke cike da kwantsa.

Yace."Wai meye hakane? ki saki jikinki kina tare dani babu abunda za suyi miki."

Ta kalleshi hawayen bakin ciki na zuba tace." Ba zan fita a motar nan ba sai ka sallami wa'innan 'kazaman dasu da karnukansu bana  san ganinsu.

Yaji haushin maganarta amma sai ya basar!  kawai ya bud'e 'kofar ya fita.....aikuwa karnukan ne suka dinga tsalle suna rungumeshi! akwai  sabo mai tsanani a tsakaninsu.  takaici da bakin ciki ya ishe ta, kullum yana kiran kansa musulumi amma yana tu'ammali da karnuka wanda kowa ya san hakan haramun ne a musulunci.

Alba ya kwance masa bakin wani kuttu dake cike da tsumi!!! sai kumfa yake!! ya kafa kansa ya dinga kwankwad'a!! yana wata irin girgiza!

Gurin cika yayi manya da yara duk sun kewayeshi alamu dai sun nuna jama'ar garin suna alfahari dashi.

Duk bada'kalar da take faruwa tana kallo, duk rokon da tayi masa hakan bai sa ya fasa abinda yayi niyya ba, kafaffar wu'ka gayawa jini na wuce! ya kar'ba a hannun Alba tana walwali ya fara dadurawa! a wuyansa! anci sa'a wannan karan bai cire rigarsa ba. ya kai minti goma yana gurzawa wu'kar! kafin ya kurma! uban ihun! da ya sanya gurin amsawa! ya fara kai kawo a gurin yana dukan kirjinsa!

Takaici yasa kawai ta sunkuyar da kanta 'kasa bata tsammanin zata iya cigaba da kallonsa yana wannan halin.

Farar shaddar jikinsa ta rine! tayi jajawur! ta jike da gumiin jikinsa! hatta! da gashin kansa digar da gumi! yake!

Kawu Ado ne yayi namijin tunkarar gurin da yake! yana kokarin rike hannunsa yana fizgewa! jin karfi kawai yake yana wani tattaune bakinsa, su kuma yaran sai kara kambaba darajarsa suke suna 'kara tayar masa da tsumin da yake jikinsa.

Maigari da jama'arsa suka 'karaso gurin domin suna zaune a fada labari ya samesu cewa *GOJE!* ya shigo garin.

Maigarin ya samu nasarar isa gurin da yake......Kawu Ado ya rufa masa baya. dukkaninsu *mubaya* (goyon baya) sukayi kafin ya sadadu! Maigari da Kawu Ado hannu na dukan hannu 💪🏻suke masa kirari! *Cau!! Sa'a dai!! Mai maganin wuka da kaho."!!* ire-iren wannan kirarin suka dinga yi masa kafin su samu kansa! jagab! ji'ke da gumi suka rirrik'eshi domin shiga dashi cikin gidan.

Cikin uwar dakin Uwale Kawu Ado ya zaunar dashi, kafin ya fita ya sallami yaran nasa da har yanzu ba su daina bushe-bushe da buga gangani ba, garin duk ya hautsine! sai kace wani babban basarake ne ya sauka.

Da sauri- sauri yake sauke numfashi makogwaronsa sai suya yake, a maimakon yaji sha'awar ruwan sanyi amma abun mamaki a lokacin babu abunda yake bukata face hayakin Sigari ko shisha duk dai wanda ya samu.

Sai da ya dan samu nutsuwa tukkuna ya fito, aikuwa ya tarar tsakar gidan cike da mata 'yan uwa da kuma abokanar arziki.

Kaf ya dube gurin babu ita babu dalilinta.

Gabansa ya fad'i! ya kalli Uwale da fadin." Ina Zinatu."?

Tace." Umaru ai kai zan tambaya ni da na barka tare da ita a mota."

Ba tare da ya sake wata magana ba ya kama hanyar fita......matan dake tsaitsaye a gurin sai gaisheshi suke da kyar yake iya amsawa, gabadaya hankalinsa na gurinta.

Tunda ta hango fitowarsa daga gidab ta dauke kai tare da jan tsaki! cikin ranta take ayyana wasu abubuwa a kansa.

Ya bud'e motar idanuwansu suka had'u! bai ta'ba jin kunyarta ba irin yau!

Yayi saurin janye idonsa yana dawurwura domin ya ma rasa me zai ce mata.

Ganin haka ya sanya kawai ta girgiza kanta ta fara kokarin fitowa daga motar. ya dauki handbang d'inta ya rike yana gyara mata hijab din dake jikinta.

Cikin gajiya ta fito daga motar tana dudduba gurin.

Ya rufe motar da fadin." Muje ko."? Gaba yayi tabi bayansa kamar bata son taka 'kasa.

Handbag din ya mika mata da fadin." Ki shiga zan shigo yanzu."?

Kallonsa tayi na minti biyu kafin ta girgiza kai da fadin." Ni ba zan shiga ni ka d'ai ba."

Bai ce mata komai ba ya koma gurin motar ya bude ya dauko Shishar sa dake cikin kwali! ba ta gane komeye ba amma tana ta kallonsa gami daso ta hasaso abunda yake cikin kwalin.

Ido ne yayi caaaaa! a kanta yayin da suka shiga gidan......Wa'inda basu santa ba tambaya kawai suke "Wannan ce matar UMARU."? Uwale na basu amsa daidai da abunda suka tambaya.

Ita dai kasa tsayuwa tayi kawai tabi bayansa dakin da taga ya shiga.

Hamra'u na dakin sai share-share take.......Yanayin dakin ya nuna nasa ne tun lokacin

samartaka  duba da irin tarin kayan farauta da suka rataye a bagon  dakin da kuma tarin buhun-buhun magungunan gargajiya irin wanda yake bayarwa.

'Kura duk ta tashi a dakin sakamakon rashin gyaran da bai samu ba tsayin watannin da suka wuce.

Taja ta tsaya bakin k'ofar tana mata wani irin kallo,  wallahi bata ta'ba ganin mara zuciya irin ta ba, kullum cikin bautar namijin da babu guarantee akansa.

Ganin yaki mata magana yasa ita ta magantu tace." Kin ga ya isa haka don Allah! mutumin da ba zama yazo ba meye zaki damu kanki gurin gyara masa daki, ko kin manta yau zai tafi."

A sanyaye  Hamra'un ta kalleshi wai ko zaiyi magana, Uffan bece ba shima so yake ta fita ya samu sararin busa hayak'insa.

Jiki babu kwari tazo za ta wuce da tsintsinya a hannunta, hanya ta matsa mata har yanzu kallon shashasha take mata, to idan ba haka ba akan me zata dinga wahalar da rayuwarta.

Ta fita daga d'akin ya fito da shishar ya fara tada hayaki!

Ta kalleshi da fadin." Ni ce marainiyar wayonka ko."?

Ya kalleta tare daso tayi masa karin bayani.

Murmushin takaici tayi kafin tace." Ka b'oye ashararanci da kake a idon duniya saboda gudun abun magana amma da yake ni ka mayar dani towon tushe baka jin kunyar aikata abu mara kyau a gabana."

Ya fesar da hayakin dake bakinsa kafin yace." Kwalbar giya ki ka gani a hannuna."?

Tayi shuru tana kallonsa

Yace." Wannan da yake  hannuna! bashi da lada ko zunubi!  sanya kai ne ga wanda yake da ra'ayi kuma bana sha sai irin haka ta faru, ko kin ta'ba tsintar karan Sigari a aljihun rigata."?

Ba tace komai ba tana dai ta nazari da tunani a kansa.

Yayi murmushi da fadin." Ko kin manta kalmar da take cewa (Mata sirrin miji) kece sirri na kuma ina da ta tabbacin cewa duk rintsi duk wuya zaki rufa min asiri a kowane hali, akwai bambanci sosai a tsakaninki da Hamra'u."

Maganganunsa suka kashe mata jiki, ta dinga kallonsa tana sake jin kaunarsa na ratsa sassan jikinta.

Da hannu ya nuna mata kusa dashi da fadin." Zo ki zauna kusa dani  sanyin idanuwana."

Murmushi tayi kafin ta nufi gurin ta zauna kusa dashi da fadin ." Dubi jikinka yanda ya 'baci! kayi wani dukun-dukun! sam wannan rayuwar ba ta dace da kai ba."

Ya ajiye abunda ke hannunsa gabadaya ya mayar da hankalinsa kanta,  yace." *ZINA* ina so ki fahimci wani abu,  wannan abun fa ya kai matakin da ba za'a iya raba ni dashi ba,  ya riga ya zama jiki da Jinina! duk sanda  tsumin ya tashi bana iya sarrafa kaina,  tun ina yaro nake shan magungunan tauri! a cikin dabbobin da Allah ya hallita masu rai kad'an ne ban ci ba. nayi gwagwarmaya da jinsi mutum da aljanu domin har so sukayi su bude min ido! ni ne ban bada goyon baya amma duk da hakan wani lokacin idan sun so suna ziyartata muyi hira su tafi salin alin ba tare da sun cutar dani ba.... babu tabbas akan aljani kuma ba'a yarda dasu amma ni bana tsammanin cewar zasu cutar dani da duk wanda ya shafe ni, dalili musulmai ne kamar yanda nake musulmi saboda haka ki kwantar da hankali kisa a ranki cewa ni ne abokin rayuwarki."

Gabadaya jikinta ya mutu jin abinda yake fada........Dama ta jima tana zarginsa cewa bashi kadai yake rayuwa ba akwai masu taimaka masa.

Ta rasa wane irin tunani za tayi a kansa.

Yace." Bayan sallar la'asar za mu tafi gida bana tsammanin barin ki a garin nan."

Wani bala'in dadi y rufe ta, amma bata nuna masa ba tace." Saboda me."?

Shu'umin kallo yayi mata kafin yace." Ba zan iya bacci ba yau saboda sha'awar dake damuna kwana biyu kina fushi dani kin daina kwana a dakina."

Sunkuyar da kanta tayi tana wasa da yatsun hannunta.

Hannu yasa ya daga fuskarta,  wanda yayi daidai da shigowar Hamra'u dakin tana sheda masa

ruwan wankan data dora masa yayi zafi."

Hankalinsa gabadaya yana kan matarsa ya amsa da" Okey to na gode kanwata."

A sanyaye ta saki labulan d'akin,  zuciyarta kamar ta fashe sakamakon abunda ta gani a tsakaninsu.

Yana fitowa daga wankan Uwake ke sheda masa cewa Kawunan sa suna son ganinsa......Yace." Babu damuwa yanzu zai shirya yaje ya samesu.

Ya shiga dakin ya sameta a kwance saman katifarsa sai juye-juye take cikinta ne yake ciwo  ga yunwa na damunta.

Cikin kulawa yace." Zina akwai abunda ke damunki amma idan na tambayeki sai kice babu komai."

Tana ya mutse fuska tace." Ciki na ne yake ciwo idan ba amai nayi ba to  ba zan ji dadi ba.

Girgiza kansa yayi da fadin." Sannu Allah ya sawwake me kike bukata idan na fita na kawo miki kin san  muna da komai na gargajiya."

Tace." Goba da mangaro amma irin wa'inda basu nuna ba."

Yace." Shikkenan."?  shuru tayi na minti biyu kafin tace." Meye ma sunan abun."?

'Yar dariya yayi kafin yace." Agwalima kuke ce masa ko."?  tace." Yawwa dashi da kuma Magarya."

Yace." An gama ranki ya dad'e! amma gyad'a marau-marau fa."

Dariya ya bata kafin tace." Ina so."  Yace." To insha Allah zan kawo miki, ki kwanta ki huta yanzu ni zanje gurin. Iyayana suna nema na.".

Tace." To babu damuwa a ce ina gaishesu."  Yana kokarin fita ya amsa da zasuji insha Allah."

Yayi wa Uwale sallama lokacin tana kicin tana aikin soye-soye......da yake  tana da irin kaji na hausa wanda take kiwo a can baya, sai ta bar su a hannun Tasallah shine fa  tasa aka yanka

mata guda biyar aka gyarasu tsaf ta kawo mata tare da duk abun bukata...

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*103&104*
Su biyu ya same su zaune a cikin rumfar kwanon dake k'ofar gidan Kawu Adon, a nutse ya cire takalmansa kafin ya hau kan tabarmar ya zauna cikin girmamawa suka gaisa da juna tare da tambayar bayan rabuwa.........Kawu Haruna yace." Bayan rabuwa sai alkairi Umaru abubuwa da yawa sun faru masu dadi da marasa dadi sai godiyar Allah dama kuma haka duniyar take yau da gobe duk na Allah ne."

Yace." K'warai hakane Kawu Amma naji dadin ganinku cikin koshin lafiya babu wata matsala wannan ne dalilin da yasa hankalina ya kwanta sosai dan idan ba dole ba, babu yanda za'ayi nayi nesa daku to kana taka Allah na tasa tabbas hukuncin da Allah ya zartar shine dai-dai."

Kawu Ado yace." Umaru mu ai hakan abun alfahari ne a gare mu, domin ka fita zakkah a cikin mu, nasan yanzu da yawa wa'inda suke zagin ka a baya jikinsu yayi sanyi domin bahaushe yace (Dan hakin daka raina shike tsone maka ido) kuma Ubangiji na saukar da ikonsa sai dai kallo, shiyasa idan kaga wani yana aikata kuskure babbah ko yaro ta kafadi alkairi ko kuma kayi shuru, jama'a da yawa sun kasa gane hakan, sai sanda Allah ya saukar da ikonsa tukkuna, saboda haka ka daina damuwa wai dan kayi nesa damu hakan ne alkairi a gare mu bakidaya."

Cike da jin dadin maganar yace." Masha Allah Kawu Na gode kwarai da addua da kuma fatan

alkairi Allah ya kara girma."

Suka amsa da "Ameen." kafin gurin ya dauki shuru na 'yan mintina.

Ya dan gyara zamansa da fadin." Uwale ce ke sheda min cewa kuna nema na."

Gyara zama yayi tare da gyaran murya kafin yace." Mak'asudin kiran akan wannan yarinya ne Hamra'u! kwanakin baya mahaifinta ya sameni da maganar muka tattauna kuma ya fahimce ni sosai amma na sheda masa cewa sai kazo tukkuna za'a tsayar da magana."

Yayi shuru yana nazarin maganar...sam! baya san gaggawa acikin al'amarinsa, amma yana ganin dole ya amince musu dalili bashi da kwakwkwaran hujjar da zai bayar.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ni kaina al'amarin yana damuna,  kuma na san da yawa daga cikin mutanan gari sun dauke ni kamar mara amana da cika alkawari!  tabbas Allah ke tsarawa bawa rayuwarsa amma a mafarki banyi tunanin auran wata mace bayan Hamra'u ba, akwai abinda Allah yake nufi da faruwar hakan, saboda haka yau  nake da niyyar komawa bakin aiki amma zan bar komai a hannuku duk abunda ya kamata ayi  na neman aure a tabbatar an gabatar zan turo kudin hidima da sauransu idan yaso sai a tsayar da lokaci."

Gabadayansu farin ciki ya lullubesu dama babban burinsu ace yaron ya dawo gida yayi aure, domin auran da yayi a baya sam bai kwanta musu a rai ba  sai kuma gashi had'uwarsu ta farko da sukayi da yarinyar ta nuna k'yama! a garesu wannan shine dalilin da yasa gabad'aya suka d'ora mata karan tsana basa kaunarta ko kad'an.

Kawu Haruna yace." Allah yayi maka albarka Umaru  yanda kayi mana biyayya Allah ya azurtaka da yaran masu albarka, Allah ya jikan mahaifinka yayi masa gafara."

Ya amsa da "Ameen ya Allah Kawu Allah ya saka da alkairi."

Kawu Ado yace." Yanzu kai ya kamata ka tsayar da lokaci domin mu shedawa mahaifin yarinyar."

Yayi jim!  yana nazari kafin yace." Shekara guda yayi."

Kawu Haruna yace." Haba Umaru wane irin shekara kuma? me ka nema ka rasa da har zaka ja lokaci haka."

Shuru kawai yayi yana kallonsa shi a ganinsa shekarar shine dai-dai lokacin matarsa ta haihu hankalinsa zai fi kwanciya baya so yanzu ta samu labari matsala ta afku.

Kawu Adon yace." Kayi shuru kana tunani Umaru ka duba lamarin nan da kyau."

Yace." Kawu akwai dalilin da yasa nace a sa shekara guda domin iyalina na da juna biyu kasan mata da kishi bana so wata matsalar ta biyo baya idan ta samu labari."

Kawu Haruna ya 'bata fuska tsanar yarinyar ta sake nunnukuwa a ransa yace." Umaru na dauka ai tuntuni ka shedawa matarka tsakaninka da yarinyar nan Hamra'u, ai bai kamata kaja bakinka kayi shuru ba tunda tilas ta san ba zata zauna ita kad'ai ba."

Ya tsirawa Kawun nasa ido yana mamakin furucinsa.....Idan ban da kaddara baya tsammanin kara aure domin bai tashi da ra'ayin haka ba, mace daya ta isheshi rayuwa mutukar ta cika abunda yake bukata, amma yanda ya tsara rayuwarsa ba haka Allah ya tsara masa ba, wannan shine dalilin da yasa yake mamakin furucin kawun nasa.

Kawu Haruna yace." Wata shida za'a sanya shine dai-dai."

Yace." To shikkenan Kawu Babu damuwa Allah ya tabbatar mana da alkairi."

Gabad'aya suka amsa da "Ameen ya Allah."

Ya d'an gyara kafin yasa hannu cikin aljihu ya fito da kudi 'yan dubu-dubu saffi kar guda ashirin ya ajiye gabansu da fadin." Ga wannan babu yawa bayan haka akwai kayan abinci a can gidan Uwale idan na koma yanzu zan sanya yara sukai gida."

Suka dinga godiya suna shi masa albarka gabadaya bakinsu yaki rufuwa sai fatan alkairi suke masa. sallama yayi musu kafin ya bar gurin cike da tararrabi da damuwar abunda zai biyo baya.

Kawu Ado ya shiga gidansa bakinsa kamar gonar audiga.

Matarsa Taburni tana tsintar shinkafa ta kalleshi tana mamakin annushuwar da ya shigo dashi gidan

Kusa da ita ya zauna da fadin." Kina da labarin zuwan Umaru ko."?

Tace." Eh na samu labari a bakin yara Allah yasa da alkairi yazo mana."

Ya fito da sabbin kudin ya ajiye a gabanta, ta dauka tana lissafawa ta kalleshi da fadin." Dubu goma ne."

Yace." Kwarai kuwa haka ya bani ya kuma bawa Haruna sannan yace yanzu zai turo mana da kayan abincin.

Ta washe baki da fadin." Kai masha Allah ashe yau za muyi miya da nama! mun gode sosai Allah ya saka masa da alkairi."

Ya amsa da "Ameen yana tattara kan kudinsa yasa a aljihu da fadin." Bayan haka kuma mun tsayar da magana wata shida masu zuwa za'a daura auransa da Hamra'u 'yar gidan 'kawarki 'Dayyiba.

Taburni ta rangad'a bud'a farin ciki kamar ya kasheta tace." Lallai Allah yayi aure da mara kwabo! yanzu kuwa zan je na shedawa kawata halin da ake ciki."

Yace." Ai yanda na lura da yaron kamar yana tsoron matarsa ne idan ba haka ba mai zai sanya yace sai ta haihu sannan za'ayi maganar aure a take a gurin Haruna ya nuna masa fushinsa.

Taburni ranta a bace tace."Au! ciki ne da matar tasa."?

Yace." 'Kwarai kuwa ciki ne da ita har yayi kwari mana."

Taja tsaki da fadin." Hegiyar yarinya mara mutunci ai duk sanda na tuna abunda tayi mana sai raina ya 'baci! bana k'aunarta ko kad'an ."

Yace." Duk cikinmu babu mai k'aunarta! wannan ne dalilin da yasa muke so yayi auren cikin gida domin mu samu wacce zata mutuntamu ta kuma daraja mu."

Tace." Wannan shine gaskiya, naji dadin faruwar wannan al'amarin, Allah kuma ya tabbatar da alkairi." Ya amsa da "Ameen." Yana kokarin kishingida a gurin.

Ita kuwa da sauri ta tashi ta fara aikace-aikacen ta tana Allah-Allah ta kammala taje ta shedawa 'Kawarta albishir mai dadi.
Da wata iriyar kasala ya koma gidan, gabadaya kansa ya daure ya rasa wane irin tunani zai yi.

Bacci take sosai duk gumi ya ji'kata! da sauri ya dage labulan ya dora saman 'kofar dakin, kai tsaye dakin Uwale ya nufa ya samo mafici ya fito wanda yayi dai-dai fitowarta daga kicin, ta

kalleshi da fadin." Har ka dawo."?

Yace." Eh yanzu nan na shigo Zinatu taci abinci."?

Tace." A'a ai bayan fitarka  na leka dakin sai na sameta tana bacci, shine dalilin da yasa ban tasheta ba.

Yana kokarin barin gurin yace." Yanzu zamu shirya tafiya insha Allah."

Kallo ta bishi da kallo tana mamakin maganarsa.

Rigar jikinsa ya cire ya zauna kusa da ita tare da kokarin cire mata rigar jikinta.

Ido ta bud'e cikin alamun bacci take kallonsa. sai ta fara kokarin tashi zaune.

Ya taimaka ta tashi  burinsa kawai ya rabata da rigar saboda gumin da take.

Ha nashi tayi domin tsarguwa tayi ganinsa babu riga sai take tunanin wani abu zai yi mata.

Da ya fuskanci haka sai ya girgiza mata kai da fadin." Babu abunda zanyi miki ki cire rigar saboda zafi.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta fara kokarin tashi........hanyar fita ta nufa ya bita da kallon mamaki!

Bandaki ta shiga ta kama ruwa kafin ta fito ta daura alwala.

Uwale ta fito daga kicin hannuna rike da farantin  silba da kwanukan abinci a jere, ta kalleta da fadin." Kin tashi kenan."

Murmushi kawai tayi ba tare da tace komai ba ta fara kokarin kar'bar kayan abincin.

Ta janye da fadin." A'a ki bar shi na k'arasa lada na mana."

Murmushi tayi tana kallonta, hakika matar nada kima da daraja a idonta.

Ta ajiye Tire din da fadin." Umaru ashe sai da ka tashi yarinyar nan ."

Yace." Uwale tashin shi yafi alkairi  tayi sallah ta kuma ci abinci  domin mu dauki hanya da wuri.

Tace." Tun dazu kake magana a 'boye  me kake nufi ne."?

Yace." Uwale kiyi hakuri tare zan koma da ita."

Ta 'bata rai da fadin." Okey ta saka ka a d'aki ta nuna maka rashin yarda ta kenan." Maganar tayi dai-dai da shigowarta dakin.

Itama Uwalen sai da ta fadi maganar sannan kuma tayi dakace.

Yace." Ko d'aya kawai nayi wani tunani ne, shiyasa na sanja shawara."

Ba tace komai ba ta kama hanya ta fita ranta a 'bace!

Tana idar da sallar ta kalleshi da fadin." Ka bari kawai zamu dawo tare dasu kayi tafiyarka."

Yace." Saboda me? shin kin san damuwa da nake ciki kuwa."?

Tace." Kayi hakuri ka danne damuwarka duka kwana nawa za muyi zamu dawo."

Shuru kawai yayi mata a ransa sam beso hakan ba dan dai sun fi karfinsa ne.

Tare suka ci abincin sai jifanta yake da wani irin kallo na mussaman wanda ya kashe mata jiki babu shakka akan ga'ba yake tana jin tsoron suyi abun kunya.

Aikuwa dai abunda yake shirin faruwa kenan, dan fafur! yaki tafiya lokacin yayi kwanciyarsa sai bayan da ya biya bukatarsa tukkuna! kunyar duniya ta isheta, ba ta iya wanka a lokacin ba sai da ta tabbatar cewa duhu yayi sannan ta tsarkake jikinta ta gabatar da magariba da isha'i......Lokacin shi kuma ya gama shirin tafiya.

Zuciyarta ce ta karye ta kasa kallonsa sai kokarin mayar da hawaye take.

Koda ya fuskanci halin da take ciki sai ya rungumeta yana rarrashinta......Yanzu bashi da damuwa tunda ya kawar da abunda ke damunsa.

Sosai ta b'oye damuwarta duk dan kada Uwalen ta fahimci wani abu ta saki jikinta sosai! suka dinga hira a tsakaninsu. Har take tambayar Hamra'u, nan take sheda mata cewa ta tafi gidansu a can zata kwana.

Allah sarki Uwale mace mai karamci da kanta ta gyara mata shimfida sabon zanin gado ta shimfida akan gadon katifar audigar dake shimfide akan gadon karfenta irin na mutan da , ta

kunna mata turaran wata na tsinke! dakin ya dinga kamshi mai dadi,  bata kwanta ba sai da tayi wanka tukkuna ta sanya wata doguwar riga cotton mai tausa sai tasa hula da yake duk tayi gurizin abinda zata bukata....Sosai taji dadin kasancewarta a d'akin, tayi kwanciyarta kan lallausar katifa iskar hadari na kad'a labulan dakin.

Mijinta kawai take gani a lokacin da idonta yake lumshe, ta kira wayarsa ba adadi taki shiga da alama  gidan bashi da network ko kad'an ! gabadaya ta shiga damuwa, muryarsa kawai take bukatar saurara a kunnanta.

*Ayi hakuri da rashin posting akan lokaci wallahi  kanwata ce za tayi sauka al'kur'ani Gobe🙏🏻*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*107&108*
Sai gefin magariba ta tashi daga baccin daya d'auketa,  jiki babu kuzari ta tashi zaune da sunan Allah a bakinta, shiru tayi tana tunanin irin wuyar da tasha a d'azu,  tabbas da kwananta ya 'kare babu wanda ya isa ya hana Allah zartar da Allah ikonsa, sam ba tayi tsammanin cewar zata sake wata rayuwar ba, duba da irin siradin data tsallake, a mai da gudawa  ba karamin cuta bane,  yanzu ma gabad'aya bata jin dadin jikinta,  duk yayi laushi akwai bukatar karin ruwa a tare da ita.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke ta fara kokarin sauka daga gadon,  kira ya shigo wayarta dake saman gadon,  ta dauka tana dubawa,  a kalla ya kira yafi sau ashirin tana bacci, tausayinsa ya rufe ta, tasan yana can a dame kamar yanda take a takure!  ko kuma jikinsa ne yake fada masa cewa akwai matsala.

Ta daga wayar cike da so  taji muryarsa, network yayi tsiya dan sai magana take masa amma shi ba yaji.....Ta kashe wayar ta sake kira anan  ma ba babu biyan bukata, kamar zata fashe da kuka ta ajiye wayar takaici duk ya isheta.

Uwale ta shigo dakin,  ganinta a zaune yasa ta sauke ajiyar zuciya tace." Kin tashi ko ya jikin naki."?

Tayi kokarin danne damuwarta ta amsa da fadin." Naji sauki sosai na gode."

Tace." Haba ai babu godiya a tsakaninmu Gimbiya Allah dai ya kiyaye gaba."

Ta amsa da "Ameen ya Allah."

A sanyaye tace." Amma don Allah ina neman alfarma a gurin ki."

Cike da mamaki take kallon matar wace irin alfarma ce."?

Tace."Don Allah kada ki fad'awa mijinki abunda ya faru kinji ko."?

Murmushi kawai tayi kafin tace." Insha Allah kada ki damu ba zan fad'a masa ba."

Tace." To na gode sosai."

Har ta juya zata fita daga dakin ta dakatar da ita....."Ina bukatar nayi wanka jikina bana jin dadinsa."

Tace." Ai dole!  amma kiyi hakuri ayi sallah tukkuna bari na dora miki ruwan zafi sai ki gasa jikinki."

Tace." To shikkenan hakan yayi." Uwale ta fita daga dakin tana godiya ga Allah ganin yanda ya gajarta musu wahala.

Cikin ikon Allah ta na yin wanka jikinta ya warware   ta zauna taci abinci zuciyarta fes domin ba tayi tunanin cewa wai abincin da taci dazu ne ya janyo mata matsala ba,  itama tafi tunanin

cewa ko sauyin yanayin gari da  sauransu.

Ta kalli Uwale da fadin." Ina so nayi waya amma gidan nan bashi da network yana bada matsala."

Tace." To yanzu ya za'ayi kin ga yanayin gidajen namu ginin da ne babu tsayin katanga a daki ga zurfi.

Tace." Zan fita waje ko Allah zai sa a dace."

Tace." To shikkenan  babu damuwa.

Can wani fili ta nufa,  duk da dare ne hakan bai hana gane ta ba, ido yayi caaa! a kanta, yara da manya masu wuce wa.

Ita dai bata damu ba bukatar ta, ta samu wayar masoyinta.

Bugu daya ta shiga ya daga, abun mamaki tar taji muryarsa babu gargada.

Ajiyar zuciya mai sanyi ta sauke kafin tace " Darling  ya kake? ina fatan kana cikin koshin lafiya."

Yace." Kin san hakan ba zata samu ba, ZINAT me yasa baki  d'aga wayata  akan lokaci ba."

Tace." Ba laifi na bane network ne babu a garin, nima na damu da kai sosai wannan dalilin yasa na fito waje wani fili duk dan naji muryarka."

Yace." Yanzu kina nufin ba'a cikin gida kike ba."?

Tace." Eh ai cikin  gidan na fad'a maka babu network mai kyau.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ki koma gida bana san tsayuwar ki a gurin nan."

Tace." Haba babu fa abunda zai faru duk ga jama'a nan suna kai kawo a gurin."

Ajiyar zuciya ya sauke  yana tunanin  wani abu a ransa,  jiya kwana yayi yana munanan mafarkai a kanta, amma yasan babu wani mahalukin da ya isa ya cutar da ita face Allah ya

mayar masa da sharrin kansa.

Hamra'u da k'awarta Zabbah  suka hangota a tsaye da waya a kunne.

Hamra'u tace." Zabbah ga mutsiyaciyar can."

Zabbah ta kalli gurin da fadin." To me ya fito da ita a wannan daran ita ba 'yar gari ba."

Tace." Waya ta take na san kuma da masoyina take, yau sai naci  mutuncinta in yaso duk abinda zai faru ya faru."

Zabbah ta rike hannunta da fadin." Hamra'u kada fa ki aikata abunda zai janyo miki matsala ki bi komai a sannu a hankali."

Ta fizge hannunta da fadin." Zabbah ni kad'ai na san irin b'akin cikin da wannan matar ta k'unsa min, ai magana ta 'kare tunda manya sun shiga maganar har an tsayar da ranar daurin aure."

Hannunta ta fizge ta durfafi gurin da Gimbiyar take tsaye....Zabbah ta rufa mata baya.

Tace." Darling zan shiga na kwanta sai da safe." Daga d'aya b'angaran yace." Okey Allah ya tashe mu lafiya amma ki mika min gaisuwa gurin babyna kafin mu had'u."

Tana murmushi tace." Zai ji da kyau! amma shima yayi kewarka sosai.

Yace." Haka nake so ai duk sanda muka had'u zamu gaisa sosai ki bashi hakuri."

Cikin shagwaba tace."  'Daya babyn naka ma yana bukatarka fa."

Ya lumshe ido tsigar jikinsa na tashi! ya gane abinda take nufi shiyasa gabadaya kasala ta rufeshi yana bala'in son yanayin shagwabarta.

Yace." Wannan babyn yayi min laifi ki sheda masa cewa idan muka had'u zan hukuntashi da kyau."!

Ta fashe da dariya da fadin." Ba ruwana  amma na yarda duk sanda kuka  ka had'u kayi  masa hukuncin da ya dace."

Yana sake release a kujera yace." Zan kuwa cire masa kai shine hukuncin da zanyi."

Maganar ta bata kunya sosai  tana 'yar dariya tace." Ni dai sai da safe."

Yace." Dole ki gudu mana kin san halin da ki ka jefa ni ciki kuwa."?

A sanyaye tace." Kayi hakuri gobe ka dauki azimi."

Yace." Azimin dole kada kiyi  tsammanin gani na gobe kuma idan nazo komai rigimarki tare zamu tafi."

Tace." Ai gobe ne bikin idan kazo sai mu tafi shikkenan."

Yace."Okey Allah ya kaimu amma mybe shigowar dare zanyi.

Tace." To idan hakane kawai ka bari sai jibi da wuri sai ka shig.......maganar ta katse sakamakon zuwansu Hamra'u gurun.

Ta kashe wayar tana kallonsu.

A wulakance tace."  Munafukar Allah ta ala to duk asirin da kuke Allah ya karya alkadarinki, ina so ki san cewa baki isa ki hana abinda Allah ya hukunta ba."

Cike da mamakin maganarta tace." Ke wannan wace irin magana ce."?

Da yatsa ta nuna ta kamar zata tsone mata ido tace."  Hamra'u  ta UMARU ce  shekara da shekaru ina nufin ke baki isa ki shiga tsakanin masoya ba."

Sai abun ya bata dariya amma ba tayi ba ta dake ta sha kunu da fadin." Kin san ni nafi karfin kiyi min rashin kunya ko."?

Aikuwa sai ta fusata! ta sake nuna ta da hannu da fadin." Ke asuwa kuma?  ko kin dauka kina da mutunci a garin nan,  to bari kiji dake da kare! baku da maraba domin bama 'kaunarki, kuma ki kwana da shirin wata shida kacal ya rage a daura min aure da mijinki   sai kiyi duk abinda za kiyi."

Ranta ya 'baci  sosai da irin fitsarar da yarinyar take mata, kawai sai ta girgiza kai ta kama hanya domin barin gurun.......Tace." Matar cushe bata daraja."!!

A fusace! ta juyo ta wanke fuskarta da mari wanda sanya ta ganin gilmawar taurari!   ta dafe gurin cikin kad'uwa da mamaki take kallonta.

Ta nuna ta da hannu tana so tayi magana, amma tsabar b'acin rai ya  ha nata furta komai, kawai ta girgiza kai a gaggauce ta bar gurin, zuciyarta kamar ta fashe saboda tsananin bacin rai!

Zabbah ta kalleta da fadin." Ko babu komai kin sha mari! wallahi Hamra'u baki da wayo har yanzu."

Ido jawur! take kallonta kafin tace." Kin san Allah Zabbah!  sai na rama mari na don kutumar ubanta tazo cikin garinmu ta mare ni, wallahi ba zan yarda ba." Fizge hannunta tayi ta nufi cikin gidan.

Zabbah ta bita da kallon takaici tana girgiza kai  kwata-kwata Hamra'u bata da wayo wallahi, kishi hauka take,  ai idan itace ba zata fito da kishinta a fili kowa ya  fahimta ba,  amma ita duk inda ta zauna maganar kenan,  tayi ta zagin Gimbiyar

Kai tsaye da ta shiga gidan kanta ta nufa gadan-gadan!  mari ta kai mata, tayi saurin kaucewa ta mari iska!! ta tsaya tana numfarfashi idonta cike da ruwan hawaye take fadin." Wallahi baki isa ki mare ni na kyale ki ba, sai na rama." Ta sake mika hannu da niyyar marin ta, kafin tayi aune! taji saukar wani  lafiyayyan marin a fuskarta!

Uwale hankali a tashe! ta shiga tsakaninsu tana tambayar ba'asi.

Gimbiyar ranta a 'bace  tayi mata bayanin duk abinda yake faruwa.

Uwale ta kalli Hamra'u da fuskar bacin rai tace." Amma wallahi kinji kunya Hamra'u kin 'bata wayonki ban ta'ba tunanin haka zuciyarki take ba sai yau."

Sai kawai ta fashe da kuka takaici biyu ya dameta, na farko tasha marika masu zafi daga gurin Gimbiyar, gashi bata samu sararin ramawa ba ana fada mata bakar magana, dama ba tun yau ba ta gane cewa Uwalen tafi kaunar Gimbiyar a kanta.

Bakin ciki da takaici ya ha nata magana kawai ta  kada kanta ta kama hanyar fita tana share hawaye.

Zabbah dake tsaye a tsakar gida tabi bayanta tana rarrashinta....."Yanzu idan Umar din yaji abinda ki kayi wa matarsa kina tsammanin zai kalleki da  mutunci? Hamra'u shifa yaki dan zamba ne me yasa zaki 'bata rawar ki da tsalle."

Ta daga mata hannu da fadin." Kin ga Zabbah na gaji da jin wannan maganar taki, domin ta kunan hagu take fita, kin san Allah sai na saubata matar nan! sai ta gwammace kida da karatu."

Zabbah tace." Yawwa to dama tuntuni ta wannan hanyar ki ka biyo yafi sauki idan kin bi ta karkashin kasa babu wanda zai fahimce ki, amma kin zauna kina hauka haba Hamra'u!

Mugun tsaki taja mai tsayi fuuuuuuu! ta shiga gidansu ba tare da tayi mata sallama ba, girgiza kanta tayi itama ta kama hanyar gidansu cike da mamakin al'amarin.

Malam Shafi'i yana dawowa Dayyiba ta shirya masa karya da gaskiya cewa yana da kyau yaje har gidan Uwalen ya tauna tsakuwa dan aya taji tsoro domin ba zai yuwu ace 'yar uwar tasa tana fifita wata a kan jininsa ba.

Aikuwa ya dauki zugar matarsa domin ransa ya baci da jin abinda 'yar uwarshi ciki daya tayi wato tana fifita wata a kan 'yarsa

Har gida yaje ya sameta ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba, sai kumfar baki yake yana sakin kausasan maganganu wanda duk wani mai hankali ya auna maganar ya san habaici ne.

Tana daga cikin daki duk ta na jin abinda yake faruwa....Uwalen na share hawaye tace." Shafi'i na gode da cin mutunci matarka ta zuga ka kazo har gida kaci mutuncina cikinmu daya da kai, baka duba furfurata ba, ka tsaya a kaina kana fada min magana babu komai na gode."

Yace." Ai gaskiya na fada miki Uwale ki gyara kuskuranki, kafin ki k'aunaci kowa Hamra'u ya kamata ki nunawa kauna da kulawa, amma a karon banza kin watsar da zumunci saboda kwadayi kin kama wata mara tarbiya kina mata ladabi a gabanki ta fitar da hannu ta tsinkawa yarinya mari ki kasa daukar mataki, karshe ma ki ka mayar da laifin kanta, wannan ba adalci bane."

Ta sanya gefan zani ta goge ragowar hawayen da ya rage tace." Tabbas da na san wannan bacin ran zan samu da nayi zamana banzo ba, Shafi'i ban ta'ba tunanin akwai ranar da za tazo ka tsaya a gabana ka nayi min rashin kunya ba."

Yace." Duk abinda nayi miki ke kika janyo idan kina son zumuncinmu ya cigaba da gudana to kiyi gaggawar sanya albarka a cikin auran Umaru da Hamra'u! domin da kin so da tuni Umaru ya auri yarinyar nan idan da rabo a kusa ma da tuni ta haihu."

Tayi shuru ta kasa magana tsabar bacin rai!

Shi kuwa rigarsa ya buge ya fita daga gidan ransa a bace.

Tana daga cikin dakin take jin sautin kukanta, tausayinta ya rufeta,duk akan ta nuna kulawa da ita ne yasa aka zo har gida aka sanya ta zubar da hawaye......ita kuwa zata bawa mara da kunya. taji wani kwarin gwiwa a tare da ita.

A nutse ta zauna a kusa da ita tare da dafa kafad'arta.

Ta kalleta a sanyaye da fadin." Kiyi hakuri abinda akayi miki kinji ko."

Girgiza kanta tayi da guntun murmushi a fuskarta tace." Uwale ke zan bawa hakuri nasan dalilina dan uwanki yazo har gida yaci miki mutunci iya son ransa, kuma cikin maganganunsa na fahimci abunda yake nufi. Ban hana Umar Auran Hamra'u ba, nima kaddara ce ta had'a ni dashi ashe shine uban 'ya'yana ban sani ba, Amma wallahi kaf tunanina bai ta'ba kawowa cewa zan aureshi ba ballantana har na fuskanci matsala irin wannan, wallahi na amince ya auri yarinyar nan mutukar shine kwanciyar hankalinku gabadaya.

Uwalan ta dinga kallonta tana mamakin furucinta, sam ba tayi tsammanin cewa tana da sauki kai irin haka ba, yarinyar nada nagarta sai mu'amula ta had'aku sannan zaka fahimta.

****

Washe gari da sassafe ta fita wajen gidan domin samun network......Lokacin jama'a basu fara kai kawo ba, ta kira shi yana shirin fita.

Cike da farin ciki ya daga wayar "Farin ciki na kin tashi lafiya."?

Ta amsa babu yabo babu fallasa kafin ta d'ora da fadin." Za kazo yau din."?

Yace." Eh insha Allah, ina fatan lafiya."? ba tace masa komai ba, kawai ta kashe wayarta ta koma gidan.

Ta samu Uwale ta fito da shirin shiga gidan Tasallah........Tace." Na fita ne nayi waya da maigidanki yace yana kan hanya insha Allah."

Tace."Allah ya kawoshi lafiya da dai nayi niyyar mu zauna mu kwana biyu amma saboda abubuwan da suke faruwa na rashin dadi gwara mu tafi shi yafi alkairi."

Murmushi tayi wanda ya tsaya iyakacin fatar bakinta, tace." Wancan kayan dake cikin baggo na tsaraba ne ya kamata tunda zaki shiga cikin jama'a ki tafi dasu."

Tace." Kina nufin akwai wasu kayan da ki kazo dasu."?

Tace." Eh suna can dakin." tafada tana nuna dakin Umar din da yake dake rufe.

Uwale kasa magana tayi saboda mamakin mutunci da karamcin yarinyar, tana da kyawun zuciya tana kuma da kyauta da alkairi hakan kamar a jinin jikinta yake.....Ta kalleta da fadin." Sannu da kokari, Allah ya saka da alkairi amma yana da kyau muje tare dake sai ki basu da hannunki.

Tayi jim tana nazarin maganar kafin ta girgiza kai da fadin." Babu komai Uwale ni dake duk daya ne kawai ki basu a matsayin kece ki ka kawo musu babu komai."

Tace." Aa ba za'ayi haka ba, idan ma ba za kije ba babu damuwa amma tabbas da sunanki zan bada kayan."

Tayi murmushi da fadin." To hakan ma yayi ni zan shiga na kwanta Allah ya sanya alkairi." Ta amsa da ameen tana kokarin bude dakin Umar din domin fito da kayan.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*